[12/15/2016, 10:48 PM] Mss Mjay💅: *WRITTEN BY MSS MJAY*💃
In dedication to *Sembyy luff(TWEA)*

*01*

Sauri sauri gudu gudu take tafiya,tanayi tana waigen bayanta domin ta tabbatar in bai biyo ta ba,ta riga ta gama tsorata da halin mahaifinta,ace ka haifi mutum amma ka nuna kashi ya fishi matsayi a wurinka.Wannan dame yayi kama,da ana chanja mahaifi data dade da chanja nata tunda baya sonsu daga ita har kannenta da mammyn su.Tana cikin tunanin nr harta qaraso makarantar tasu mai suna COLLEGE OF ARABIC AND ISLAMIC STUDIES, tana zuwa bakin gate ta hadu da kawarta mai suna hafsah a tsaye tana jiranta.Suka rungume juna cikin farin ciki tare da karasawa cikin makarantar.

Karfe 3:00 daidai aka tada su,suka jero suna tafiyan su itada hafsah.Da hafsah taga shirun yayi yawa kuma kaman yau ran qawar tata a bace yake.

A hankali tace"taybah Ifya kike kuwa yau,you seem lost in thought,ko abbu ne kuma?"

Taybah ta juyo a hankali ya kalli kawar tata tare da qoqarin goge kwallan daya taru a idonta tace"ki bari kawai hafsah,abbu nada matsala ni banma san ya zanje in samu su mammy ba yau"ta fada cikin kasallaliyar murya".

"Kiyi hakuri taybah,Allah yana tare daku,ungo wannan inkin koma gida ko gari ki siya muku kusha" ta fadi haka tare da miqa mata 100.

Taybah tayi dariyan farin ciki tare da runguma kawar tata cikin farin ciki"i love you bestiee na,nagode sosai".Daidai nan suka qaraso kofan gidansu hafsah ta shiga ciki tare da ma qawar tata sallama.

Taybah taci gaba da tafiya cikin sauri ta qarasa shagon tanimu ta siyo musu garin 70 sugarn 30 ta qarasa gida cikin farin ciki.

Koda ta shiga ta samu mammy zaune tayi tagumi su kuma su yasmeen na zaune kusa da ita,daga gani sunci kuka harsun gaji.Suna ganinta suka ruga da gudu suka rungumeta"Oyoyo addah taybah,kin siyo mana wani abune?"salimah ta fada tana qoqarin karban ledan hannun yayar tata.

Taybah tayi murmushi tare da miqa mata ledar garin ta qarasa wurin mammyn tasu tana gaida ita.suna cikin gaisawa ne yasmeen ta dawo ta roba ta zubo garin tare da spoons.Suka fara sha har mammyn tasu amma ita spoon 3 kawai tayi ta bar musu saura.

"Mammy kisha mana"taybah ta fada cikin tausayi."karki damu taybah cikin nawa ne banajin dadin shi,kusha kawai"ta fada cikin murmushi.

Taybah ma bata sha garin sosai ba ta tashi ta shiga daki.ta tube kayan jikinta tana neman na sawa idonta yakai kan wata takarda da mammyn tasu taketa boyewa tuntuni.

©Mss Mjay

[12/15/2016, 10:48 PM] Mss Mjay💅: WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG
WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

*KUNDIN KADDARA*

WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NGWWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

Written by
*MSS MJAY❤*

In dedication to
*sembyy luff*

WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG
*02*

Daukan takardan tayi a hankali tare da boyewa a cikin kayan da zata sa.

Ta fito daga dakin ta zauna kusa da mammy sannan tace "mammy inaso inje gidansu hafsah na manta government note book dina a hannun ta gashi gobe munada test".

"Toh shykenan taybah, karki dade dan Allah dan inaso inje gidan hajiya hussai kozan samu wanki inyi".
"Karki damu mammy, yanxu zan dawo in shaa Allah".

Tana cikin tafiya kawai saita tuno takardan data tsinta a daki daxu. Tayi sauri ta lalubo cikin zanen ta tare da fito da takardar. tana budewa taga an rubuta

"Ni usman bada yawuna ba in kika..........."
Tana cikin karantawa ba tare data lura cewa ta karaso bakin titi ba kawai taji mota tayi sama da ita!.

WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG
8
Matuqin motar ya fito cikin sauri tare da tabata amma ko motsi kadan batayi ba. Yana cikin dubata ne takardar da take karantawa ta fado daga hanunta.
Ya dauka tare da sawa cikin aljihun shi sannan ya juya a fusace yana kallon dan nashi dake tsaye kawai yana kallon su.

"Zaka dauke ta ne kasata a motar kosai ranka ya baci".

Cikin hanzari matashin saurayin ya duqa tare sa daukan ta sannan ya nufi motar da sauri. Ba bata lokaci suka nufi asibiti "JOS UNIVERSITY TEACHING HOSPITAL" (JUTH) dake hanyar lamingo.

Suna isa aka wuce da ita emergency cikin sauri.

Alhaji usman ya dubi dan nashi cikin bacin rai yace....
"Bansan randa zakayi hankali ba faysal, kana tuqi amma bazaka lura da abunda kakeyi ba?

Faysal ya duqar da kanshi sannan yayi magana a hankali "Kayi hakuri daddy, fadan daka mun ne duk ya gigita ni wallahi".

Saboda takaici kasa cemai komai dad din nashi yayi.

Sun kusa 40mins a zaune sannan likitan dayake dubata ya fito.
"Are you her father?"  Ya furta yayin dayake kallon alhaji usman.

Alhaji usman yayi sauri amsawa "yes i am.....i hope everything is alright doctor".

"Come with me".......likitan ya fada sannan yayi gaba.
Alhaji ya bishi da sauri tare da addu'an Allah yasa komai lafiya.

©Mss Mjay
[12/15/2016, 10:48 PM] Mss Mjay💅🏽:
WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NGWWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG
*KUNDIN KADDARA*
🎈🎈🎈🎈🎈WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

Written by
*MSS MJAY❤*

In dedication to
*sembyy luff*

WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG
*03*

Suna shiga office din likita ya dubi alhaji usman tare da cewa."mr?".

"Usman please",  ya fada cikin sauri.

"You look tensed mr.usman, don't worry your daughter is perfectly alright" likitan ya fada cikin murmushi.

Ajiyan xuciya alhaji usman yayi tare da hamdala.
"Can we see her please?".

"Sure you can, we can discharge her as soon as she is awake". Likitan ya fada.
"Thank you doctor". Alhaji usman yayi gaba faysal na binshi a baya Suka shiga dakin da take ciki. Tana kwance tana bacci cikin nitsuwa ba tare da wata damuwa ba.
Alhaji usman ya dubi faysal tare da fadin
"Zanje gida,ka zauna da ita in an sallameku da wuri ka kaita gida kama iyyayenta bayani".
"Toh shyknn dad".

WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

*4hrs later*

"Yasmeen, nikam ko zakije gidansu hafsah ki dubu addahn ku, tun dazu ya kamata ace ta dawo amma har yanxu shiru kakeji". Mammy ta fada cikin bacin rai.
"Kila wani abu ta tsaya yi mammy amma bari inje in gani"

Tana cikin tafiya ta hadu da hafsah a hanya. Da sauri ta qarasa tare da tambayanta addahn ta.
Hafsah ta dubeta cikin mamaki sannan tace
"Dama tace wurina zataje ne?".
"Ea addah hafsah, kuma yanxu kusan 4hrs kenan bata dawo ba shine mammy tace inje in dubota". Yasmeen ta fada cikin sauri.
" Toh aii yanxu gidan naku zanje in kai mata notebook dinta". Itama hafsah ta fada. "Muje wurin mammy kawai". Ta sake fada sannan suka juya suka nufi gida.

Hankalin mammy ya tashi sosai jin wannan labari. Har bayan wasu 2hrs ba taybah ba dalilinta gashi kuma abbansu ya kusa dawowa, hafsah harta gaji da jira ta tafi gida.

Tana cikin tunanin ne tajiyo sallamarshi yana shigowa gidan. Da sauri ta miqe tana jiranshi ya qaraso.
Ya shigo gidan da ledarshi a hannu. Su yasmeen duk suka gaishe shi. Ko kulasu baiyiba balle mammy ta take qoqarin karban ledan hannunshi.
Yayi saurin ture hannun nata tare da fara fada "bance ki dinga boye yaranki a daki ba daga na shigo?kin kama kin haifo yara mata kawai, me zasu mjn inba qarin wahala ba. Ina yar iskar yarki take, tazo ta dafamun indomien nan ta soyamun kwai ta kayo mun daki ina jira.
"Taybah! Taybah!! Taybah!!!, ya kira a fusace.

"Malam tun dazu ta fita amma har yanxu bata dawoba, dama in jira ka dawo ne ko zaka dubo mana ita". Mammy ta fada a tsorace.

"Kice kawai kin turata yawon iskanci"
Ya wurgo mata ledan hanunshi tare da fadin
"Gashinan kije ki dafa ki kawo mun, wannan matsalar kuce".
Yayi gaba abunshi ya barsu tsaye suna sharan kwalla.

WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

*10:00pm*

A hankali ta bude idonta tana tunanin abunda ya faru, da sauri ta miqe tana dube -dube idanunta ya sauka akan faysal yana gyangyadi.
A hankali ta ce "bawan Allah".
Ya juyo a hankali tare da mata murmushi "kin tashi?"
Ya furta a hankali. "Bari in kira likita ya sallamemu koh".

©Mss Mjay
[12/15/2016, 10:48 PM] Mss Mjay💅🏾: 🎈🎈🎈🎈🎈WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG
*KUDDIN KADDARA*
🎈🎈WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

Written by
*MSS MJAY❤*

In dedication to
*sembyy luff*

WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

*04*

Cikin yan mintuna ya daeo tareda wata nurse,ta duddubata sannan ta basu sallama.

Faysal ya matso kusa da ita tareda kallonta,sai yanxu ya kare mata kallo dakyau.

Taybah doguwar yarinya ce,baqa amma irin baqin nan mai sheqi, tanada manyan idanuwa masu kaman an diga musu zaiba(sexy eyes)with long eyelashes a pointed nose da bakinta dan qarami(kaman na hafsy😂😜).

Tanada dire sosai ga baqin gashinta dan daidai.

Jin shiru yayi yawa yasa taybah dago idonta domin taga meke faruwa, Dago idon dazatayi ta sauke su akan kyakyawar fuskar shi mai cike da kamala da haiba.

Dogo ne wankan tarwada. Awwn he's damn handsome (mummy ki rufe baki hakanan plzz😂).

Kawar da fuskarshi yayi sannan ya qara juyowa ya kalleta yaga she's lost in thought staring at

him. Yana daga cikin abubuwan daya tsana kallo dayawa.

Nan da nan yaji ranshi ya baci har baisan lokacin daya mata magana a fusace ba
"Ki tashi mu tafi kin tsaya kallona, ko yau kika fara ganin kyakyawan saurayi ne?"
Ya fada raising one of his eyebrows and feeling a little bit irritated.

Taybah taji wata kunya ta rufe ta, tayi saurin dauke kanta tareda sa hijabin ta. Tayi tsaye tana jiran mai zai ce kima.

"Ki wucr mu tafi mana"
Ya fada cikin fada.

Tayi gaba da sauri har tana tuntube ya biyo ta a baya suka qaraso harabar asibitin.

Suna isa gaban motar wayan faysal yayi kara, ya ciro wayan tareda da duba me kiran sai yaga dad dinshi ne.

"Salamu alaykum dad, yanxu aka sallamemu zan kaita gida ne"

*No son,ku jirani gani nan xuwa nida umman ka, don't go anywhere".
"Lfya dai koh dad?" Faysal ya tambaya adan tsorace.

"Son just wait for us" alhaji usman ya fada tareda katse wayar.

Faysal ya juyo yana kallon taybah, daga gani ta gaji da tsayuwar da take a wurin.

Ya bude mata bayan motar tare da fadin "kizo ki shiga kafin dad ya qaraso" yayi maganar kaman ana sashi dole.

Taybah ta tako a hankali tana dafe kanta inda ta bugu, jiri takeji kaman ta fadi a wurin.
Ji tayi jirin nata ya qaru saura qadan ta fadi taji taba kirjin mutum.

Dago kan da zatayi ta daurasu akan fuskarsu, kasa motsawa sukayi suka xubama juna ido.

Taybah tayi inhaling turaren da faysal ya fesa soo deeply.

Wannan ai saita suma, irin wannan kamshin haka damn! He's more handsome yanxu.

Shi yayi saurin dauke kanshi tare da taimaka nata ya qarasa da ita cikin motan yana fadin
"Banason ana kallon mun handsome face hake, wannan kallo aii sai kisa kyauna ya qare ya fada ba tare daya dago kao ya kalleta ba.

Taybah ta kautar da kai cikin jin haushi, sai kace shima ba kallon nata ya tsaya yi ba.

She can't deny the fact that he's handsome, but that doesn't give him the right to be arrogant.

She was deep in her thought har batasan lokacin da alhaji usman ya qaraso ba.

Sai jin muryarshi tayi yana fadin "faysal shiga kaja tana nuna maka hanyar gidan nadu xamu biku a baya".

Faysal ya dubi dad din nashi yanason yayi tambaya yana tsoron fadan shi.
Sai kawai ya fada motan tare da mata key ya dauki hanya.

Taybah na nuna hanya har suka qaraso anguwan nasu.

Tun daga nesa ta hango abbu yana cin wani abu a takarda.
Ta nuna ma faysal wuri tarw da cemai yayi parking anan kawai.

Kafin ta samu daman fitowa ta hango dad da sauri ya qarasa wurin abbu.
Dago kan da abbu xaiyi suka hada ido.

A firgice ya furta "ya usman"

©MssMjay
[12/15/2016, 10:48 PM] Mss Mjay💅🏾: 🎈🎈WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG
*KUDDIN KADDARA*
WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

Written by
*MSS MJAY❤*

In dedication to
*Sembyy luff*

WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

*05*

"Ya usman kaine?"
Abbu ya sake furtawa a firgice.

" ina samyrah?"
Shine kawai abunda Alhaji usman ya iya tambayan shi.

"Tana cikin gida,bari in kirata"

"A'a barta kawai, abunda yasa nazo yanzu dama dan kawai in tabbatar in kudin ne or akasi aka samu. Toh amma yanzu tunda na tabbatar zan wuce gida da waccan yar taka gobe zan turo a dauke ku da safe".
Alhaji usman yayi maganar yana nuna Taybah.

"T..to..to yaya, Allah ya kaimu goben".
Daga gani abbu a tsorace yake sai zare ido yake(kaman randa na kama maman nawal na tadi da saurayina😏).

Alhaji usman ya juya tare da kallon mu mu ukun sannan yace
"Faysal, shiga mota mutafi gida".

"Wuce ki bishi ku tafi tamana"
Alhaji usman ya furta ganin Taybah batada niyan binsu.

Taybah ta daga kai tana kallon Abbun nata ya watsa mata harara tare da mata nuni da hannu akan ta bisu.

Sum sum ta juya ta shiga motar, faysal ma ya karaso ya shiga.

Alhaji usman harya kama murfin motan zai shiga sai ya sake juyuwa yacema abbu
"Af abubakar, karka cema samyrah komai har goben".

Kada kai kawai abbu yayi su kuma su Alhaji usman sukayi gaba.

Taybah kuka kawai takeyi, meyake faruwa ne? Ta tambayi kanta, ai da sun bari ko mammy ta gani tukunna anzo kuma an sake hadata da me shegen kallon nan.

In yanzu ya kalleshi yace ta fiye kallo. Mtsswww taja wani dogon tsaki wanda har yayi sanadin da faysal din yaji.

"Keh, ince dai badani kike tsakin nan ba?"
Ya tambaya angrily dan tsaki in one of thd things he hate soo much.

"To ni ko kallonka nayi ne? Ina ruwanka dani wai?".
Ta fada tana turo baki.

Amma wannan yarinyar akwai yar iska ya fada cikin ranshi, zanyi maganinki amma.

Kowa da tunanin dayake har suka qaraso wani tafkeken gida dake *rayfield*.
Ma shaa Allah Taybah ta furta cikin ranta daidai lokacin da faysal ya gama parking din motar.

Ta fito tayi tsaye a wurin shi kuma faysal ya wuce ciki ya barta nan.

"Zoki wuce ciki mu tafi koh"
Mahaifiyar faysal ta fada tare da dafata.
Koda suka shiga falon sai suka sami faysal akan dining sai gwabza loma yake.

"Ya sunanki?"
Matar ta sake mata magana

"Taybah"
Ta furta a hankali tana sunkuyar da kai.

"Taybah ki saki jikinki damu, ni nan da kike gani yayan mahaifiyarki ne, wannan kuma matata ce".
Ya fada yana nuna hajiya karimah.

Da sauri Taybah ta dago kai tana kallonshi, dama da rabon suga wani danginsu a duniya?
Take taji hawaye na zubumata ba kakkauta.

"Allah nagode maka"
Ta fadi hakan tana rungume Ammi.

"Mtswww"
Faysal yaja wani dogon tsaki tareda da barin dining din ya doshi side dinshi cikin sauri.

Binshi da kallo kawai sukayi sannan Alhaji usman ya kada kanshi kawai yayi gaba tareda fadin......

"Ki kaita dakin rufaida nada ta kwanta ta huta, gobe duk zamu warware komai in shaa Allah".

Hajiya karimah tayi yanda yace tareda da sa Taybah tayi wanka, ta bata rigan baccin sannan ta debo mata abinci ta mata saida safe.

Koda Taybah ta gama ta kwanta saita kasa baccin, tunanin fuskan faysal kawai takeyi tana murmushi.

"Yeah, he's handsome, especially eyes nashi. OMG su sukafi komai kashe ta.
Ta murqusa tare da juyawa dayan bangaren taci karo da hijabinta, nan da nan kamshin turaren

faysal ya mamayeta....ta rungume hijabin inhaling the scent har qamshi yayi awon gaba da ita.

WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

*8:24am*

"Kin shirya?"
Ammi ya tambayi Taybah bayan ta qaraso dakin.
"Ea ammi, amma rigan ta matse ni sosai"
Taybah ta fada tana qara gyara rigar tata.

Murmushi Ammi tayi taja hanunta suka nufi dining tareda fadin...
" zamuje wurin tailor gobe in shaa Allah".

Suna sauka idanunta suka sauka cikin na faysal dayayi mutuwan zaune yana kallon ta.

He's soo lost in her thought har baiyi noticing time din da suka qaraso dining din ba.

Tsinkayo muryarta mai sanyi kawai yayi tana gaida dad, sannan ta juya ta gaida shi kaman bataso.

Ya amsa a yatsine yana wani kawar da kai.

"Laaa, yaa faysal, wannan ce budurwar taka daka cemun tazo jiya? Whoa ya she's beautiful".

Taybah ta tsinkayo wata zazakar murya tana fadin haka, sai lokacin ta lura ashe akwai yarinya ya kimanin 10yrs old a zaune a wurin itama.

Ammi ce tace "ki gaida ita mana ummu, she's your elder sister"

"Amma zatayi iya auren ya faysal koh?"
Ta cigaba da surutun ta kaman ba cewa akayi da gaida ita ba.

Tsawa faysal ya daka mata tareda fadin "dallah ki rufema mutane baki koh"

Sum sum ta wuce cikin jikin taybah da sauri tare da boye fuskar ta ajikin ta.

Dad ne yayi gyaran murya yana fadin....
"Ya isa hakanan, kowa yaci abinci, faysal inka gama kaje gidansu taybah ka dauko mun iyayyenta".

"Toh dad".

Ya riga kowa barin dining din sannan yayi gaba, taybah ta bishi da kallo admiring his outfit.

Yana sanye cikin shadda fara ras data sha aiki ash colour, yasa hula ash colour and a black swatch.
O Allahna!, ta fada a ranta holding her breathe, what the hell is wrong with her?.

Sun gama breakfast suka zauna a nan main parlor suna jiran faysal su qaraso.

Can sai kawai suka tsinkayo sallamar faysal abbu na biye dashi sannan mammy dasu yasmeen.

Kana ganin mammy kasan hankalinta ba'a kwance yake ba.

Tana dago kai suka hada ido da alhaji usman.

Cak ta tsaya ko motsi ta kasa yi. Ta saje murxa ido tana kallon alhaji usman har yanxu.
Cikun karfin hali ya furta....

"Ya usman, kaine kuwa"?

*©Mss Mjay*
[12/15/2016, 10:48 PM] Mss Mjay💅: WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG
*KUNDIN KADDARA*
WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

Written by
*MSS MJAY❤*

In dedication to
*sembyy luff*

WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

*06*

"Ya usman"!

Mammy ta sake furtawa a firgice tare da fashewa da wani kuka mai ban tausayi.
"Ya isa samyrah, ba kuka zakayi ba, yanxu duk ku zauna muyi magana" cewar Alhaji usman.

Duk suka zauna, an dauki kusan 20mins ba wanda ya iya cewa komai.

Alhaji usman ne yayi qarfin halin fara magana

"Nayi nadama safiya, nayi nadaman abunda ya faru shekarun baya, kiyi hakuri"
Ya juya ya dubi su faysal da suka zubamai idanu suna kallo kawai.

Murmushi kawai yayi sannan yace "nasan kun matsu kuji abunda ya faru....yanxu kuwa zan fada muku"

*26yrs back*

"Asalin mu yan garin kaduna ne, a anguwan kanawa. Mahaifinmu riqaqqen malami ne, amma hakan bai hanashi samu makarantar boko ba. Daga ni sai samyrah Allah ya mallaka musu. Mahaifiyar mu inna tayi qoqari wurin bamu tarbiyya mai kyau har muka girma.

Bana taba mantawa,lokacin ina university of jos(uj)....na gama 200lvl nazo hutu gida na samu malam kwance baida lfya. Babu yadda banyi dashi ba akan mi kaishi asibiti yaqi sai umurni daya bani na inje gidan limamin anguwan mu a daura mana aure da yarshi....shine kawai abunda yake buqata.

Haka na tafi bawai dan na santa ba kona taba ganin ta...a'a sai dan inma mahaifina biyayya.

Aka daura mana aure da karymah ta tare a wani dan bangare na gidan.

Haka nayi hutuna malam baida lfya. Na koma da sati daya rasuwar malam tazo mun.
Nayi kuka,nayi kuka amma bashi zai dawo da malam ba.a lokacin samyrah ta gama junior secondary school amma bataci gaba ba.

A kwana a tashi harna gama karatuna na kuma samu aiki saina dauki karymah muka koma jos....ba yadda banyi da inna akan tazo muje tare taqi.saina barta tare da samyrah a lokacin tana shekarar tabta karshe a secondaru school.
Inada ya daya lokacin wato rufaida wadda a halin yanxu tana aure a abuja.

Shekarata biyu da komawa jos inna ta rasu. Sai na dawo da samyrah gidana nan jos muka zauna.
Kwatsam saiga kabir yaxo, dane ga yayan babanmu wai yazo neman aure samyrah, ba yadda banyi da ita ba akan karta aureshi tace ita shi take so.naji haushi a lolacin faysal nada shekara daya da yan watanni.

Naji haushi nacema samyrah babu ni babu ita domin kabir baida mutunci ita kuma ta dage.
Hakan kuma bai hanani mata kayan daki ba suka zauna a kaduna a anguwan rimi, na bata jarin kudi tareda wasika nayi gaba.tun daga ranar ban qara waiwaiyar rayuwarta ba, a cewata tunda ta batamun rai babu ni babu ita.
Takardar dana bata ita na tsinta ranar dana kade taybah. Ta haka harna gano inda kuke.
Kiyi hakuri samyrah, ki yafewa wannan yaya naki kuskuren shi".

Alhaji usman ya qarasa bada labarin yana kuka.

Falon yayi shiru bakajin motsin komai Sai kukan alhaji usman da samyrah.

"Yaya kayi hakuri...naga kaddara iri iri bayan rabuwar mu....amma na godema Allah daya sake hada fuskokin mu".

Shidai malam kamal yayi mudus, ya kasa cewa komai.

"Toh kamal, so nake ka barmun taybah a hannuna, zan riqeta". Cewar alhaji usman.

"T..tt..toh ba komai yaya, yanda kace haka za'ayi". Malam kamal ya amsa.

Faysal kuma haushi yaji, shi dad dinnan ya rasa wadda zaice a bashi sai baqar yarinyar nan.
Taybah ma tunanin ta kenan, yanxu shyknn ya faysal zan dinga ganinshi kullum.
Tana cikin tunanin ne ta tsinkayo muryar dad yana tambayar ta aji nawa take a school

"Ss3 abbah, saura sati biyu mu fara waec" .

Ta amsa shi a nutse.
"Toh shyknn, in kin hama exams sai faysal ya kaiki abuja wurin rufaida kusan juna koh".cewar alhaji usman.

Aka watse taro Ifya su mammy suka tafi gida bayan sunyi lunch a gidan.

*8:04pm*
Taybah ta fito daga kitchen cikin sauri tana jera abinci a kai, ta sake komawa ta dauko 5-in one friut juice datayi.

Sannan ta haura sama cikin sauri tayi wanka tareda sake wata red arabian gown da ammi ta bata daxu. Rigar me robace gashi tabi jikinta tayi das.

Bata shafa komai a fuskanta ba sai kawai tayi rolling kanta da baqin gyale, ta fesa arabian pef dinta"oud al-abha" sannan ta fito.

Tana saukowa falon ta hadu da faysal shida abokin shi a azaune suna hira, dad da ammi kuma na dining a zaune suna jiransu.

Gani tayi kaman ya faysal ya qara kyau, looking soo muah cikin wani black wando da white top wadda ta fito mai da shape din chest dinshi.....(woo koni na fola balle maman nawal😊😜).

Taybah shagala kawai tayi da kallon shi ba tare data lura shima kallon nata yake ba.

Ba make-up ne a fuskan ta tayi kyau haka😳??tabb!!! Yayi maganar a cikin ranshi.
Sai tsinkayo muryar abokinshi yayi yana cewa "abokin who's this charming damsel?? Dan Allah in yar uwarka ce ka bani ita". Ya fada witjout taking his eyes off her.

Faysal bai samu damar ansawa ba yaji dad na cewa "kuzo muci abincin mana".

Taybah tayi saurin wucewa ta barsu a gurin tare da kara rikita suda kamshin pef nata😂😂😂😂.

*©Mss Mjay*
[12/15/2016, 10:48 PM] Mss Mjay💅🏾: WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG
*KUNDIN KADDARA*
WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

Written by
*MSS MJAY❤*

In dedication to
*Sembyy luff*

WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

*07*

Taybah ta qarasa dining din tare da gaida dad da ammi, sannan ta fara serving dinsu.

"Faysal, kuzo muyi dinner mana". Cewar ammi ganin basuda niyyar miqewa.

"Barshi kawai ammi, anjima zanci yanxu zamu dan fita ne". Faysal ya fada tareda miqewa.

"Jira yaruwarka ta gama cin abinci kuje can gidan ta dauko uniform dinta and wasu abubuwa da take buqata". Dad ya fada ba tare daya dago kai daga cin abincin shi ba.

Kafin faysal yace komai ummu talkative(kaman hafsy) tayi saurin magana "Dad nima zan bisu". Ta fada tareda barin dining din gaba daya ta koma wurin faysal wai karsu gudu su barta.

*Monday....7:16am*

Taybah na hango tana saukowa da sauri cikin shirinta na makaranta. Wando baqi tare da farar riga da farin hijab dinta tayi das.
Ta tarar da ammi a dining tana jera breakfast din da taybah tayi.
"Yi maza ki karya kafin yayanki ya fito....daddynku ya riga ya fadamai shi zai dinga kaiki makaranta". Ammi tafada tana serving dinta itada ummu.
"Ai wallahi nima ya ne zai dinga kaini". Ummu ta fada tana turo baki🙄.

Taybah tayi murmushi kawai batare data ce komai ba. Kanta a duke a kasa taji wani irin kamshi ya ratso falon.
Da takalman shi ta fara cin karo yana saukowa daga steps cikin sauri.
Tana dago kai ta sauke idanunta fes suka sauka a kanshi. yana sanye cikin suit baqi ta red shirt a ciki...ga turtle neck tie dinshi.(awwwnnn....he's just soo handsome harna fola❣😍)

Ya qaraso dining din tareda aje briefcase dinshi a gefen shi sannan ya zauna. Taybah ta gaida shi tareda miqewa dan tayi serving dinshi.
"Kin gama kallon nawa kenan" ya fada absent mindly.

Ummu tayi caraf tace "Laaa ya faysal, kaima fa ina kallonka lokacin da kaketa kallon ta. Aunty rufaida ma kafin ta auri ya bello haka suke kallon nan shine dad ya musu aure, kuma aure za'a muku kenan koh yaya?.

Sake baki kawai sukayi suna kallon ummu, faysal ne yayi saurin shan toka tareda cewa
"Come on swthrt, yaushe kika ga ina kallonta, bakiga na fita kyau bane shiyasa take kallona?" Ya fada yana murmushi.

"Malamin islamiyyan mu yace bakyau qarya fa, kuma gashi kayi qarya ya faysal. Naga lokacin da kake kallonta fa. Kuma nikam wallahi Adda taybah ta fika kyau".
Taybah tace "ya isa cute sisterna, ci abincinki mu yafi school kar muyi latti koh".

Faysal ya dago ua harareta, ita kuma tamai tongue out tare dama ummu murmushi.
Su oga faysal a kiyayi aunty ummu😂😂😂😂😂.

*kuyi hakuri da wannan,am very busy ne yau. Love ya all from the beginning to the end of

seven seas❤*

*©Mss Mjay*
[12/15/2016, 10:48 PM] Mss Mjay💅: WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG
*KUNDIN KADDARA*
WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

Written by
*MSS MJAY*

In dedication to
*SEMBYY LUFF*

WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

*08*

Faysal ba gama breakfast dinshi ya tashi yayi waje tareda fadin
"Duk wadda bata fito ba tafiyata zanyi".

Ta sauri taybah ta aje spoon dinta tareda miqewa tsaye taja hannun ummu sukayi waje, koda suka fita harya tada motar shi.

Cikin sauri taybah ta qarasa tareda shiga bayan motan bayan ta budema ummu gaban motan.

Suna isa bakin gate ta hango hafsah a tsaye, daga gani cikin damuwa da fargaba take kar taybah taqi xuwa.

Ta yunkura da nufin bude motar ta fita tajita a kulle. Batare daya kalleta ba taga ya miqo mata 200 naira sannan ya cire jam lock din.

Tamai godiya sannan ta fita ta tafi. Da sauri ta qarasa wurin hafsah tareda rungumeta......"i missed you soo much yaruwa....a whole lot much".

"I missed you more hun, jiya da yamma naje gida yasmeen take cemun wai kin koma gidan uncle dinku, dagaske take ko wasa? Dan yasmeen ta raina ni wata rana". Hafsah ta qarasa maganar tana kallon taybah.

"Ki wuce mu tafi abeg, in kin fara surutu ba comma ba full stop. Am gonna gist you later about

everything". Taybah ta fada tana jan hannun hafsah suka qarasa cikin school din.

*3 months later*

Su taybah har sunyi waec dinsu sun gama. Sai jiran results.

Satinsu biyu da gama exams dad ya shirya musu tafiya abuja, tare da umartar faysal akan shi zai kaisu.

Ana sauran kwana uku dad ya bata sabuwar waya dal a kwali "iphone 6".
"Nagode dad, Allah ya saka da alkhairi ya qara budi". Taybah ta fada tana sunkuyar da kanta kasa.

"Bakomai daughter, anjima yayanku zai kaiki kima mammynki sallama ko". Dad ya fada.

Faysal yayi caraf yace "Dad, inada uziri fa, su usman suna jirana, kasa driver ya kaita kawai". Yanayi yana kawar da fuska dan karsu hada ido da taybah.

"Dad nima zan rakata, kuma gaskiya ya faysal ne zai kaimu". Cewar ummu tana tsalle.

"Dolen shi aii princesses, kyale shi kawai" cewar dad.
Sannan ya juya ya dubi faysal yace
"Ka tashi kaje ka shirya kaxo ka kaisu, daga nan ka kai taybah shopping tayi siyyaya kuma a matsayinka na babba kai zaka mata siyyayar".

Faysal ya dogo kai, karap suka hada ido da taybah ta mishi gwalo tare da juya kanta gefe.

Ammi dai na zaune tana murmushi ba tare data ce komai.

Faysal haushi ya cika shi cikin ranshi yana cewa......"Am gonna deal with this girl. Dammit, i hate you taybah".

(Kut!!, kuji malam faysal dai abeg).

*Afuwan sisters, am very busy this dayz.....kuyi hakuri......i love you all.
*Team taybah lovers😍*

*©Mss Mjay*
[12/15/2016, 10:48 PM] Mss Mjay💅: WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG
*KUNDIN KADDARA*
WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

Written by
*MSS MJAY*

In dedication to
*SEMBYY luff*

*09*

Taybah ta fito cikin shirin wata green and baby pink atampa, an mata riga da skirt.
Tayi using baby pink gyale sai yar pos din data sa wayan ta(hhh...su taybah anyi waya😂).

Tana cikin saukowa qasa ta hango ya faysal an dauki wanka, tsayawa kawai taybah tayi tana admiring dinshi.....unknown to her shima admiring nata yake.

"Laa ya, kaima kana kallon yadda aunty tayi kyau koh😊". Cewar ummu da babu wanda ya lura da tsayuwarta a gurin sai tsinkayo zazzakar muryarta da sukayi.

Da sauri faysal ya kawar da kanshi tareda jan tsaki.
"_wannan bakin naki ko princess....hmmmmn"
Yayi gaba kawai batare daya qara cewa komai ba.

Ajiyan zuciya taybah tayi sannan ta qarasa saukowa daga stairs din ta qaraso gaban ummu ta durkusa tareda cewa,
"Princess kinyi kyau....."

Ummu ta bata rai ta juya fuskanta sannan tace
"Bawani nan aunty kin fini kyau aii, gashi yaa harda kallonki ya tsaya yi. Amma ni ko kallona baiyi ba balle yace nayi kyau".......ta fada muryarta na rawa alamun tanaso tayi kuka.

"Come here princess"
Suks tsinkayo muryar faysal kamn daga dama yana ambata.

"Kinfi kowa kyau princess, who told you wancan abun ta fiki kyau, you are soo beautiful especially when you give me that big smile of yours"..........Ai nan da nan ummu ta washe her 36 jin ance tafi taybah kyau.

"Now give me five". Ji kake tasssss an kashe hannu😂.
"Toh oya wuce mu tafi". Ya fada yana jan hannunta ita kuma ta yafito taybah da tayi tsaye kawai tana kallon su.

Kuyi sorry...... School a kwana thats why.love you all❤

*©MSS MJAY*
[12/15/2016, 10:48 PM] Mss Mjay💅🏾: WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG
*KUNDIN KADDARA*
WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

Written by
*MSS MJAY*

in dedication to
*SEMBYY LUFF*

*09*

Cikin nitsuwa yake tuqin har suka qaraso kofar gidansu taybah.

Ta bude kofa a nutse ta fito sannan ta juya tana cema ummu
"Princess mu tafi ko".

A nutse take tafiya yayin da faysal ya bita da kallo harta kule.

Tana shiga ta samu mammy dasu yasmeen a zaune, ai nan da nan suka ruga da gudu suka rungume ta.

Salimah auta ta dubi yayar tata tace "adda taybah, kinga yadda kikayi kyai, nima ki tafi dani gidan uncle usman inyi kyau irin naki".
Tana fada tana taba kayan yayar tata. Taybah taji kwalla ta taru a idon ta, kafin ta samu damar cewa komai ummu tace....

"Aunty taybah yaya fa yana waje.

Sai a lokacin ta tuna tare sukazo.

Mammy ta dubeta sannan tace "dama tare kuka zo kika barshi a wàje? Wannan ai sakarci ne taybah. Kinga yi sauri kije ki shigo dashi yasmeen".

Yasmeen ta fita da sauri, cikin lokaci qanqani suka shigo tare.

Faysal ya durkusa a gaban mammy sannan ya gaishe ta.
"Ya kuka baro su yaya? Cewar mammy cikin kulawa.
"Lfya qlw mammy,sunce a gaida ku dakyau" Ya juya ya dubi taybah dake hira da yanuwanta cikin farin ciki sai dariya take.
"Sister, bari inje in dawo sai muje shopping din ko?.....before then i guess kun gama sallama".

"Ea yaya, saika dawo". Taybah ta fada cikin murna, zata je taga hafsah kenan ta nuna mata sabuwar wayarta ta kuma mata sallama.

Faysal ya ajema mammy rafar 500 tareda mata sallama ya tafi.

Taybah ta juyo cikin kulawa ta dubi mammy tana tambayarta....."Mammy, akwai improvement a halayyar baba kuwa?".

"Taybah, addu'a kawai zaku taya mahaifinku da ita, Allah ya ganar dashi gaskiya. A bar maganan kawai kinji.

"Toh mammy, Allah ya kyauta. Dama dad yace inzo in muku sallama, jibi zan tafi Abuja wurin aunty rufaida in mata hutu kafin results dinmu ya fito".

"Ma shaa Allah, Allah ya nuna mana. A jamb dinki wacce university kika cika?"....cewar mammy

"University of abuja dad yace in cika, saj in dinga taya aunty rufaida zama".

Yan uwanta suka taya murna tareda mata fatan alkhairi. Sannan tace ma mammy zataje tama hafsah sallama.

"Toh kiyi sauri ki dawo amma karya dawo bakya nan".

Itada yasmeen kawai suka tafi, suna tafiya suna hira har suka qarasa gidan nasu hafsah.

Da gudu hafsah ta fito daga daki tareda rungume taybah cikin farin ciki.

"I missed you sis, gashi ke ko yar wayan nan bakida balle mu dinga communicating".

Taybah ta harare ta tareda fadin..."huta damun gori, daxu dad ya dalle ni da sabuwar waya.

Nidai matsa mun in gaida mama tukunna".

Bata baro gidansu hafsah ba saida ta bude mata WhatsApp da facebook, su kadai taybah tace tana so. Gaba in taji tana ra'ayin wani zata bude. Sukayi exchanging contact sannan taybah ta tafi suna kewan juna.

Ta koma gida bada dadewa ba ya faysal ya daeo, tama su mammy sallama sannan suka wuce.

Sai magariba likis suka isa gida an jibgo shopping..... Aljihun ya faysal yaji pepper😂.

*©MSS MJAY*
[12/15/2016, 10:48 PM] Mss Mjay💅🏾: WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG
*KUNDIN KADDARA*
WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

Written by
*MSS MAJY*
In dedication to
*SEMBYY LUFF*

*11*

*Saturday....8:17am*

Taybah ta karasa jere breakfast din cikin sauri domin tasan any moment from now ya faysal zai fito ya fara cewa suxo su tafi.

Sausage rolls ta musu +scotch egg, sai samosa. Ta dama musu custard sannan tayi kunun gyada danta lura ya faysal na bala'in son shi.

Tana fara hawa steps taci karo da ammi tana saukowa.

"Daughter, badai har kin gama hada breakfast ba??". Ammi ta tambaya cikeda mamaki, gashi aroma ma din abincin sai tashi yake a gidan.

"Sauri nake in shirya ammi kafin ya faysal ya fito, kinsan yace da wuri zamu tafi so gwara in shirya before ya fito". Cewar taybah.

Ammi ta dubeta cikin kulawa tana yaba nutsuwarta, a ranta tana godema Allah da kuma mijinta daya kawota gidan.

"Toh shyknn daughter, jeki shirya kizo zan baki sako ki kaima yarinyar can(kunya rufaida take ji wai first born😂😂😂😂😂😂).

*40mins later*

Takun takalmi naji, daga ido nayi na hango taybah da ummu sun shaa wanka. Dukan su suna sanye da wata dakkakiyar shadda peach colour, an mata design da brown din zare.
Gashi taybah ta kashe musu dauri sun sha make-up.

Dad, Ammi and faysal duk suna zaune a falo, suka zuba musu idanu dan sunyi kyau ma shaa Allah.

Ummu ce ta qarasa gaban faysal tareda juyawa a hankali sannan tace......
"How do i look ya faysal???". Tanayi tana rangwada tana kashe eyes😂.

"Wow princess, kinga yanda kikayi kyau kuwa, i've got the most beautiful girl as a sister". Faysal ya fada yana kallonta da murmushi.

Ummu tasa tsalle jin ance tafi kowa kyau.

Dad ne ya miqe yana cewa "kuzo muyi breakfast nidai, cuz tun dazu am salivating. Daughter we gonna miss you and your cooking".

Kowa ya zauna yana cin abinci, taybah nayi tana satan kallon yayan nata sbda irin kyan data ga yayi.

Faysal ya dago kanshi da niyan qara kunun karaf idanunsu suka hadu, he couldn't take his eyes off her neither could she. They sat there staring at each other.

Taybah ce ta fara tari, i dunno ko kallon ne ta kasa jurewa harta sarqe.

Nan da nan naga faysal ya miqe tare da bata ruwa yana fadin......"take it easy sister, sannu koh".

Sandarewa taybah tayi a zaune tana mamakin wannan al'amari, ya faysal ya kulata in a loving and Caring way yau.
She just can't help but blush.....Awwn! How sweet!!!.

A tare suka gama breakfast itada faysal. Ta miqe a nutse ta nufi sama dan ta sauko da akwatin ta da mayafi kafin faysal yace su fito.

Sun qaraso parlor, faysal ya zauna ita kuma ta nufi sama.

Kamar daga sama taji faysal yace.......

"Lil sis, kinyi kyau yau". Taybah ta tsaya cak tareda juyowa ta gani koda ummu yake, amma sai taga ba kowa, daga ita sai shi a parlorn, kuma ita yake kallo.

Meaning da ita yake kenan. Yaa Rabb, ya faysal is surprising her today.

"Nagode ya faysal, ka fini kyau aii". Ta fada tana sunkuyar da kai.

"Nasani aii, basai kin tuna mun ba. Kije ki dauko duk abunda zaki tafi dashi kafin princess ta gama"......faysal ya fada yana danna wayarshi.

Taybah kasa cewa komai tayi, faysal surprise her sometimes. Wani lokaci he'll act cool and loving, the next moment he is as cold as ice. Ya faysal sucks sometimes.

Ta juya angrily ta nufi stairs. Bada jimawa ba ta sauko tana jan akwai sai uban nishi take.

"Ya faysal, kazo ka daukan mun akwatin dan please....... Tayi nauyi da yawa". Cewar taybah a marairaice.

Faysal ya daqo ya kalleta sannan yace......"nayi kamada mai daukan akwati ne, ki zaki dauko abunki ni ba abunda ya dameni".

Yana fada yayi waje abunshi a barta a tsaye a wurin.

*©MSS MJAY*
[12/15/2016, 10:48 PM] Mss Mjay💅: WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG
*KUNDIN KADDARA*
WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

Written by
*MSS MJAY*

In dedication to
*SEMBYY LUFF*

*12*

Haushi ya kama taybah, hakanan dai taita jan akwatin har ta kai waje.
Ta hango shi a mota a zaune yana waya but din motan a bude sai kawai ta qarasa tasa akwatin a ciki ta koma cikin gida.

A tare suka fito dasu dad, ummu na jan trolley qarami dan kwana biyu kawai zatayi ta dawo saboda school.

"Kayi driving a hankali plzz son, nasan halinka da son gudu". Dad ya fada yana shafa kanshi cikin kulawa.

"Zan kiyaye in shaa Allah, ku shigo mu tafi". Ya fada yana duban su ummu.

Ummu tayi sauri ta shiga baya tayi tsaye a tsakiya wai zata fi ganin titi.

Ba yanda taybah ta iya banda shiga gaban. Ammi ta leko inda take ta mika mata leda tana fadin....."in kinje ki bata, kice ta kira in mata bayani. Ku kula da kanku, sai munyi waya".

Faysal yaja motar suka bar harabar gidan. Basu riga sun fita gari ba wayan taybah ya fara ruri, ta zaro wayan daga handbag dinta.

Tana dubawa taga hafsah ce mai kira, cikin sauri ta dauka tareda fadin....."kaman kinsan kina

raina swthrt, yanxu muka dau hanya".

Hafsah tayi murmushi sannan tace "ai naji alama, keda silver-spoon yayan naki ne???".

Taybah tayi sauri ta juya ta kalli faysal ko yaji me hafsah tace, sai taga shi hankalin shi nakan tuqin dayake, ummu kuma anyi tsaye ana kallon hanya.

"Keh, sai anjima, zan kiraki inmun isa". Tayi sauri ta katse wayar tareda turawa cikin jaka.

Ta zaro littafin ta datake karantawa "are you afraid of the dark?" Na Sidney Sheldon taci gaba da karantawa.

Hankalinta gaba daya ya tafi a karatun da take kawai taji faysal ya qara gudu, gudu kuma dan kadan ba, ummu na kwance bacci ya kwasheta.

A tsorace ta dube shi tareda fadin...."wayyo ya faysal dan Allah kayi hakuri ka rage gudun nan".

Ai kamn tace ya qara kawai saiya kara ma motan kudi. Taybah aka aje littafi aka fara salati.

Suna shiga garin abuja ummu ta tashi......"yeey!!, i can't wait inga aunty rufy da sweet baby kamal and uncle saleem, ya faysal dan Allah kadan kaini sahad store in siyoma baby kamal chocolates"....ummu ta fada pleadingly.

Faysal yayi murmushi sannan yace "ki siyama kanki dai, kamal ai be damu da chocolates ba".

Ummu ta bata rai sannan tace....."inna bashi be sha bane zan sha fa". Ta fada a marairaice.

"Princess, kiyi hakuri dan Allah, na gaji amma i promise you gobe ko anjima zan kaiki.....OK?". Cewar faysal.

Ummu tayi shiru bata qara cewa komai ba har suka qaraso anguwan su rufaida dake area 8.

Aii faysal na parking din mota ummu ta fita da gudu ta nufi cikin gida da gudu tana fadin......"Aunty rufy, ki fito gani na qaraso, kizo kiga new sister na mai kyau".

Tana fada tana qarasawa cikin gidan.

Faysal ya girgiza kai yana fadin.."princess kenan".
Itama taybah murmushin tayi sannan ta fito.

Juyawar da zatayi idanunta suka sauka akan na wata kyakyawar mata, fara mai kamada ammi sosai.

Matar ta qaraso cikin fara'a ta rungume taybah...."welcome sister, naji dadin zuwanki. Muje ciki ki huta koh". Ita duk dadi ya kasheta tayi sister ta manta da faysal.

"Lallai sister, wato bakida time dina yau koh??". Faysal ya fada yana yatsina fuska.

"Yi hakuri bro, murna ta rufeni da ganin new sis dita".

Tabe baki kawai faysal yayi ya wuce cikin gida.

Suma suka bi bayanshi tana riqe da hannun taybah.

*©MSS MJAY*
[12/15/2016, 10:48 PM] Mss Mjay💅🏽: WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG
*KUNDIN KADDARA*
WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

Written by
*MSS MJAY*

In dedication to
*SEMBYY LUFF*

*13*

Koda suka shiga cikin gidan faysal direct dinning area ya wuce yana fadin.....
"Allah yasa dai favorite dina kika dafa sister". Yana fada yana bude warmers din.

Ya dago kai daga kallon warmers din yana yamutsa fuska.
"Haba sister, mene haka pls?".

Rufaida ta kwashe da dariya harda riqe ciki. Saida tayi dariyan ta mai isan ta sannan tace

"Abunda mijina yakeson ci kenan, kuma kasan banajin dadi balle ince in maka naka daban,

kayi hakuri kawai kaci da daddare zan maka kaji lil bro".

Tsaki kawai faysal yaja sannan ya fita ya nufi boys quarters inda yake sauka in yazo.

Rufaida ta dubi taybah dake tsaye tana kallon su kawai itada ummu.

"Kinga sister, muje in nuna miki dakinki kiyi refreshing kizo kici abinci koh". Rufaida ta fada tana jan hannun taybah muka nufi wani daki.

Ummu ta biyosu a baya tana cewa....."Aunty rufy, ina son kamal ne?, baze zo ya gaida second mum dinshi ba koh".

Ai su taybah basu san lokacin da suka kwashe da dariya ba, ummu bata da dama ko kadan.

Rufaida ce ta samu ta tsayar da dariyan nata sannan tace.....
"Sun fita shida dad dinshi. Amma nasan sun kusa dawowa miss second mum".

A haka suka qarasa dakin taybah, a gyara yake tsaf.

"Toh ku kintsa ku fito kuci abinci koh". Cewar rufaida.

"Toh aunty, mun gode".

Rufaida ta fita tareda kulle musu kofa, taybah tama ummu wanka sannan tasa ta tayi alwala kafin ta shiga nata wankan.

Tana fitowa ta shafa mai tareda zura wata milk colour gown tayi sallah, ummu ma ta shirya cikin wasu riga da wando masu kyau.

Kajol kawai taybah tayi alluring idanunta dashi ta yafa dan karamin gyalen gown din bayan tayi parking din gashinta.

Tana cikin gyara rolling din gyalen ummu tace mata.....
"Kinga uncle saleem koh, wata rana tsoro yake bani. Shi baya son wai in dinga surutu. Ni kuma inada baki haka kawai ace kar inyi surutu......Amma yanada kirki sosai fa aunty taybah".

"Toh naji princess, yanxu dai muje aunty rufy na jiran mu.

A tare suka fito riqe da Hannun juna, suna qarasowa parlor yayi daidai da qarasowar faysal,

uncle saleem and son kamal na ummu😂😂😂😂😂😂😂

Da gudu kamal ya nufo ummu yana mata oyoyo.
"Aunty ummuna ta zo, yau zamuyi wasa,......kuma zaki koya mun assignment dina koh?. Ya fada yana kara maqalqaleta. Sai a lokacin hankalin shi yakai kan taybah dake tsaye gefen ummu tana murmushi.

"Laaaaaa, mum waye wannan?". Ya fada yana nuna taybah.

"Nima mum dinka ce". Cewar taybah.

"Ea amma itave third mum dinka dan nice second koh son". Cewar ummu.

"Toh ya isa hakanan, in kun fara surutu ko kadan baku san ku bari ba". Uncle saleem kenan mijin aunty rufaida yake fada.

Taybah ta qarasa gaban shi ta gaida shi sannan suka nufi dinning domin aba ciki haqqin shi.

*©MSS MJAY*
[12/15/2016, 10:48 PM] Mss Mjay💅🏽: WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG
*KUNDIN KADDARA*
WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

Written by
*MSS MJAY*

In dedication to
*SEMBYY LUFF*

*14*

Faysal sai faman yatsina fuska yake yana kuma kai luma, shi a dole anyi abincin da baya so dan kawao yanajin yunwa ne yake ci......fi sabilillahi fans mene laifin tuwon shinkaafa miyan kuka harda man shanu!😂😂😂😂😂😂😂

A haka aka gama cin abinci mr.faysal na faman bata fuska.

Ya riga kowa barin dining din, yana tafe yana cewa....."gaskiya sis karki sake mun irin haka, karki sake fa...tohmn".

Taybah da rufaida suka kwashe da dariya. A fusace ya juyo yana kallon su.

Ma shaa Allah, he couldn't resist taybah's sweetness with that laughter, yeah she's cute ya sani, matsalan kawai baqa ce kuma ta cika sha mai kamshi.

"Sister kingani koh, zakisa yarinyar nan ta raina ni. jifa harda dariya take mun.

Taybah ta gumste dariyar dake cinta tana toshe baki.

"Cool down mana big bro". Saleem ya fada cikin murmushi dan shima faysal ya mugun bashi dariya.

Kasa cewa komai faysal yayi kawai saiya nema kujera yayi zaman shi yana faman huci.

Kamal ne ya taso ya biyo bayanshi yana cewa ........"small daddy, zaki kaimu sahad store wao nida small mum?".

"Na fasa kai ku, tunda aka bani tuwo miyan kuka". Faysal ya fada yana murmushi.

Ummu ta nufo su ta bata rai sosai, tana zuwa ta zauna kusa dashi sannan tace..."ka kyale aunty rufy yaa, anjima aunty taybah zata mana girki mai dadi koh sis?.

Ta fada tana kallon taybah da take nufo falon.

"Kwarai kuwa princess, sai abunda kikeso zan dafa miki yau, ki kyale aunty rufy kinji. Wait i have a better idea, muyi girki tare anjima, what do you say?. Ta fada bayan ta duqa gaban ummu dake tsaye.

"Yeeeeeeyy!!, aunty taybah is the best, yaa nafasa zuwa sahad din, yau zan maka special dish

saika cije hannunka". Cewar ummu tana wani kashe eyes😂😂😂😂

Faysal kallon taybah kawai yake yana admiring dinta......why is he always happy when looking at her????? He can't say for sure, cuz he don't really know abunda ke faruwa.

Abeg fans.....ku bashi amsa inkun sani

*©MSS MJAY*
[12/15/2016, 10:48 PM] Mss Mjay💅🏾: WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG
*KUNDIN KADDARA*
WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

Written by
*MSS MJAY*

In dedication to
*SEMBYY LUFF*

*This chapter is for you mummynah, and my crazy chuhu bae, love you guys from the moon to the back, from the beginning to the end of seven seas❤(mum phaty and Mrs Anas)*

*15*

Still dai kallon nata yake ba tare daya ce komai ba, admiring her, and having some strange feelings erupting for her deep inside❤.

Saleem nr yayi murmushi, ganin yanda su hajiya ummu aka dage yau za'ayi girki...yayi gyaran murya a hankali sannan yace...." Yau kuce girkin princess zamuci a gidan nan, na harna hango kaina ina cije fingers dina saboda dadi". Ya fada teasingly.

Ummu tayi dariya cikin farin ciki sannan tace...." Bari kawai uncle, saima kaci tukunna, aunty taybah, muje mu fara yanxu mana". Ta fada tana jan hannun taybah da har yanxu take tsugunne a gabanta.

Murmushi taybah tayi sannan tace...."not yanxu princess, let's go take a nap, anjima sai muyi koh".

"Toh shyknn, yaa faysal, buy me ice-cream please inka fita. See you guys anjima".

Suka nufi daki suka barsu zaune anan.
Rufaida ce tace....." Yau na fara haduwa da ita, amma i feel like i've known her for years, she's just soo sweet and innocent, what do you think hubby?". Ta fada tana kallon saleem dayake shan pepper soup din kayan ciki.

"Ke aii kowa is innocent to you, its too early to predict, ni haka kawai naji bata mun ba. I dunno why". Saleem ya fada in an irritating way.

Caraf faysal ya karba....." Bari kawai bro, ta cika rainin sense ne, nima haka kawai bana sonta".

Kallonsi kawai rufaida take cike da mamaki, ita bataga aibun taybah ba, tanafa hankali da nutsuwa, anyway matsalar su ce wannan. Itadai ta samu mai tayata zaman gida.

Saleem ya gama cin abincin tareda miqewa, sannan ya riqo hannun rufaida cikin kulawa yana fadin....."muje daki kiga wani abu". Suka nufi daki suka bar faysal da kamal a zaune suna kallo.

Suna cikin kallon ne taybah ta fito daga dakinsu ta nufo faysal a tsorace.

Tsugunnawa tayi dan nesa dashi sannan ta fara magana a hankali......"yaa faysal, dan Allah inka fita ka siyomun airtime, inaso in kira su ammi ne kuma phone din tawa ba airtime a ciki". Ta qarasa fada tana sunkuyar da kai kaman munafuka.

Da sauri ya kalleta a ranshi yana cewa "yarinyar nan ta gama raina shi, yau kuma shi zata aika?....tabbbb!!!."

Jin shirun yayi yawa yasa taybah dagowa ta kalleshi, sai kawai taga ba abunda yake sai kallonta, aii ba shiri ta miqe da sauri da nufin barin falon.

Tsawar daya daka mata me tayi dalilin tsayawar ta.

"Ke amma kin gama raina ni ko, inba raini ba ki dubi tsabar idona kice wai in siyo miki airtime.....ni faysal, ni zan siyo miki airtime?". Ya fada yana nuna kanshi.

Kuka kawai taybah ta fashe dashi tareda nufan dakinta da gudu, it ta rasa meyasa yaa faysal ya tsaneta haka, ita dai tasan ba abunda ta taba mai.... Amma shi kullum yafison ya ganta ranta a baci.

*8:26pm*

Hango su faysal nayi a zaune a dinning kowa diban loma kawai yake barin mr faysal😂

Babunda kakeji sai karan spoons da forks ana kwasan girkin taybah da ummu.

Taybah ta riga kowa tashi daga table din ta koma falo ta zauna, ba abunda yake damunta kaman son taji muryar mammy, gashi kuma batada airtime.

Tayi zurfi cikin tunani har batasan lokacin daya qaraso kusa da ita ba sai jin kawai tayi yace......"kije ki dauko wayar taki ki kawo mun".

Ta sauri ta dago jin muryar faysal, caraf suka hada idanu, ta mike da sauri taje ta dauko wayan.

Tana nan tsaye ya loda mata airtime din, tareda sa numbern shi a wayanta a kira tashi wayan.....(a raina nace, kome ya kaishi yin haka oho).

Karban wayan taybah tayi cikin farin ciki sannan ta nufi daki cikin dokin jin muryan mammy.

*Sunday 2:43pm*

"Toh bro, Allah ya kiyaye hanya, ka gaida su ammi da kyau". Cewar rufaida tana dafe da murfin

motan faysal.

Ummu kuma nacan cikin jikin taybah ta lafe, daga gani bata muradin tafiya tabar taybah.
Cikin lallashi taybah ta lallabata ta sata cikin mota suka tafi.

Bin mota tayi da kallo tana hawaye, there is no doubt, dukda basa shiri she's gonna miss her silver spoon bro.

*©MSS MJAY*
[12/15/2016, 10:48 PM] Mss Mjay💅: WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG
*KUNDIN KADDARA*
WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

Written by
*MSS MJAY*

In dedication to
*SEMBYY LUFF*

*This chapter is for my three most sweetest fans....Aysha shehu(maman nawal)...Sayyadah...and Ummu. I love you guys to the moon and back. Thanks for the support and encouragement. It means alot❤*

*17*

A hankali ya bude idanun nashi, tas ya sake sauke su akan taybah da har yanxu murmushin ne a kwance akan fuskan ta. Dammit! He's gonna deal with this girl today.

Cikin tsananin bacin rai ya fito daga motar tashi ya doshi su taybah..wayanda sukayi nisa a

birnin love ko dirin motar yaa faysal ba'aji ba balle asan nayi😂

Motsin da taybah taji ne yasata dagowa, fea ta sauke idanunta akan faysal. Cikin tsananin tsoro ta miqe kafin tayi yunkurin yin wani abu faysal ya kwasheta da mari, cikin fushi yace...."will you get out of my sight".

A firgice taybah ta nufi cikin gida da gudu tana kuka dafe da kuncin ta, rufaida dake kwance kan three sitter tana kallo ganin taybah kawai tayi wuf ta wuce bayanta. Tambayar duniya tayi taybah ta qasa cewa komai sai kuka kawai take.

Faysal ya juyo, fuskarshi na nuna tsantsan bacin rain dayake ciki. Cikin zafin rai ya fara cewa...."Malam,find your way out of this house kafin ranka ya baci...get the hell out!. Ya fada a tsawace.

Sakr baki kawai usman yayi yana kallon faysal, ajiyar zuciya ya sauke sannan yace....."Bansan waye kai ba, ban kuma san matsayinka a gidan nan ba, amma at least daya kamata ka tsaya kaji me nake tafe dashi, da aure nake sonta ba komai ba. Kuma ni ko gobe kuka ce in fito am ready.....you exceeded your limits by slapping her, dan kawai bansan matsayinka ba, dasai na rama mata. And believe me, i really mean it.
". Bello ya fada yana kallon cikin idanun faysal da suka chanja launi zuwa jajawur saboda bacin rai.

Kasa cemai komai faysal yayi, dan yasan zata iya kaisu ga dambe......kut! Lallai taybah tayi matsayi.

A fusace ya juya ya nufi cikin gida, ya bar bello nan tsaye.

Tun daga nesa taybah takejin muryar shi yana kiranta...."Taybah! Taybah!!...Taybah!!!...where the hell are you?...yau saikin gwammaci kidi da karatu". A haka ya qaraso falon yana sababi.

Rufaida ta miqe tsaye, yayin da taybah ta qara rakubewa bayanta tana fadin....."na shiga uku aunty rufy, dan Allah ki cece ni". Ta fada tana qara rushewa sa kuka mai tsanani.

Rufaida ta dubi faysal dayake tunkaro su cike da bacin rai, da sauri ta qarasa gabanshi ta riqo hannunshi sannan tace....."cool down bro, kayi hakuri dan Allah, kai babba ne kamata yayi ka bita a hankali....we ladies are fragile, hardai ita she's still young". Ta fada tana riqe da hannunshi.

Kwace hannun nashi yayi sannan yace...."thatz great sister, kema da kanki kin fada kince she's still young, she's just 17, har tayi guts din tsayawa da saurayi? Who gave her that right? Tun

bata je jami'a ba kenan, toh inta shiga jami'a sai yaya kenan? Tell me sai yaya?".

Rufaida da mamaki ya gama kasheta tayi tsaye kawai tana kallon faysal, kafin tace komai saiga kamal da babanshi sun qarasa falin, dama tare suka fita.

Kamal ya nufi tayah da sauri yana goge mata hawaye tareda tambayar ta..."meya sameki aunty? Dukan ki uncle faysal yayi koh?".

Girgiza mai kai kawai taybah tayi ba tare data ce komai ba.

"Meya faru ne?". Saleem ya tambaya.

"Mara kunyan yarinyar can mana na kama da wani kati wai ita tana hira...as smalk as she is tasan tayi hira da saurayi.....yau dukan tsiya zan mata a gidan nan. Gobe koda kudi akace ki kawo wani gidan nan bazaki gwada ba". Faysal ya fada cikin bacin rai tareda nufo taybah data rakube bayan kujera rungume da kamal tana kuka.
Saleem ne yayi saurin tare shi yana cewa...."Noo....ba haka za'ayi ba, tunda an mata fada shyknn abar maganan hakannan plzzz". Ya fada tareda jan hannun faysal suka bar falon.

Da gudu taybah ta fada dakinta tare da kulle kanta a cuki taci gaba da riskar kukan ta kaman bagobe.

Shi yaa faysal din an cemai tana son bello ne? Ita bataso kawai ta dinga wulakanta mutane.
Ai wallahi tunda ya daketa yau ta fara kula samari inyaso ya kasheta. Tunanin nashi ma daga yau an dena!😂😂😂😂😂

*8:25pm*

Daidai lokacin ta gama serving din kowa abinci shi. Dambun dankali(irish) tayi, sai farfesun cat fish with strawberry juice.

Tana gama zubama kowa abincin shi ta nufi hanyar dakin ta. Faysal yayi saurin juyowa tareda kallon ta, sannan a hankali ya kira ta....."Taybah, bazaki abincin bane ke?.

Juyuwa tayi a hankali ba tare data bari sun hada ido ba tace...."na koshi ne".

Kallonta yayi a tsanake yaga kamn fushi takeyi saboda marin daya mata. Sai yaji zuciyarshi ko kadan bata mai dadi ba. His priceless jewel is angry, kuma the worst part of it dashi take

fushin.........can he handle something like this?

*©MSS MJAY*
[12/15/2016, 10:48 PM] Mss Mjay💅: WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG
*KUNDIN KADDARA*
WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

Written by
*MSS MJAY*

In dedication to
*SEMBYY LUFF*

*16*

*3 months later*

Zaman taybah a abuja gwanin dadi, tana jin dadin zama da aunty rufaida, ga baby kamal mai sunan dad dinta.

Matsalan ta daya, yaa saleem, he's always finding fault in her, komai tayi sai yace bata iya ba, ko yace ta cika sanyi....blah...blah...blah....unreasonable stuffs dai.

A kuma zaman 3 months din da tayi, not a day goes by batayi tunanin faysal ba, even though be taba kira suyi mgna ba, itama bata taba kira ba.
But time to time tana waya da ummu thru his phone.

Shima faysal din bata chanja zani ba, haka yake wuni tunanin taybah, hardai sexy eyes dinta masu kashe shi inta kalleta.

Abokan shi duk sun lura faysal na cikin damuwa, sunyi tambaya harsun gaji yace ba komai.

Lokuta da dama during weekends taybah na fita da kamal....sometimes su duka har rufaida da saleem.

Amma kamar yau saturday, taybah da kamal ne kawai zasu fita.

Tana sanye cikin lace peach colour me touches na deep purple, tayi applying simple make-up dinta ta fito fes fes da ita.

Ta fito daga daki ta hango kamal da rufaida a zaune a falo, ita rufaida tana shan fruits yayin da kamal ya zaune yana jiran taybah ta fito su wuce.

"Gaskiya da alama babies dinmu zasu fito healthy, irin wannan cin fruits haka?". Taybah ta fada tana nufosu.

"Kiga twins a cikin ki madam, kajimun ya kullum kicr twins. Abeg ki bari dan Allah karya zama gaskiya". Cewar rufaida tana zare idanu.

Zama taybah tayi tareda da kwashewa da dariya sannan tace....
"Haba hajiya, ciki wata hudu amma ji yanda yayi qato, waya sani ko yan ukune ko hudu ma". Ta fada tana mata gwalo.

Mikewa taybah tayi cikin sauri ta kama hannun kamal suka nufi kofa tana dariya, dan tasan ba karamin aikin rufaida bane ta daketa.

Saida suka qarasa kofan sannan taybah ta juyo tace....."yauma ice-cream kawai kike so?".

"Ban sani ba, gaba daya oasis din zaki kwaso, zaki dawo ki sameni aii.

Gwalo taybah tama rufaida sannan suka tafi.

Saida sukaje wonderland suka bata almost 2hrs sannan suka nufi oasis.

Sun fito da ledodin su a hannu suna batun shiga mota taji wata sanyayyar murya ta mata

sallama.

A hankali ta juya ta sauke idanunta akan wani kyakyawan matashi wanda bazai wuce 26-27 years ba, dogo ne sosai amma be kai ya faysal ba,kuma dukda fari ne, yaa faysal y fishi kyau sosai(to her eyes❤)

"Wa alaikas salaam". Taybah ta amsa a hankalin sannan ta juya da nufi tafiya.

Da sauri saurayin ya tareta yana fadin......"dan Allah ki saurareni koda na minti biyar ne, please". Ya fada pleadingly.

Harde hanuwanta taybah tayi a kirji sannan tace ma kamal ya shiga mota tana zuwa.

"Ina jinka malam" ta fada ba alamun annuru a fuskarta.

"Kiyi hakuri dan Allah, na dade ina ganin ki kina zuwa nan, but i couldn't gather the courage na in tunkareki sai yau Allah ya bani iko, inbazaki damu ba dan Allah ki bani numbern wayarki, zan kiraki anjima. Bai dace mu tsaya anan muna surutu ba".

"Kayi hakuri banda waya". Taybah ta fada tana sunkuyar da kai, ita da kanta kunyar karyar data sharara take😂

Saurayin bai samu damar cewa komai ba kamal ya fito daga motan cikin sauri tareda miqama taybah wayarta dake ringing.

Tsurewa taybah tayi a wurin (wa yaga uwar nawal taga kura😂😂😂)

"Qarya bata kamace kiba yanmata, ki tausayama bawan Allahn nan ki bashi numbern....please". Ya fada yana marairaicewa.

Kunya dukta ishi taybah ta karantomai numbern. Harta juya ta fara tafiyabya tsayar da ita tareda fadin......."baki fadamun sunan ba"............. Ba tareda ta juyo ba tace "TAYBAH" ta shige mota abunta.

Suna komawa gida kamal ya ba rufaida labari yau taybah ta hadu da wani hadadden saurayi.

Koda taybah ta bata labarin qaryan da tayi suka sha dariya harda riqe ciki..

Wuraren 10:13pm wayan taybah ya fara ringing, ita harta fara bacci taji qaran wayan ta miqe a hankali tareda daukan waya.

"As salamu alaiki". Taybah taji an fada. Nan da nan ta watsake jin muryar namiji. Haka dai ta daure ta amsa

"Sunana bello ahmad amin, nine wanda muka hadu a oasis dazu, ina fatan kin ganeni?".

Sai yanxu taybah ta gane waye, a hankali ta gaida shi ya amsa sannan ya bata tarihin shi. Shi haifaffen dan garin bauchi ne, da na biyar a wurin iyayyen shi. Dan kasuwa ne shi, mussamman cosmetics na mata. Yadi zama a nan abj sbda nan kasuwan tashi tafi qarfi.
Itama taybah tayi briefing dinshi Ibrinta sannan sukayi sallama.

Kimanin sati biyu kenan da haduwar taybah da bello, kullum maganar dayace dai, taybah ta bari yazo gida su gaisa.

Yauma tana zauneba falo itada rufaida suna hira sia gashi ya kira. Rufaida tayi dariya tana cewa "nasan glue dinki ne ya kira ko".

Murmushi kawai taybah tayi tareda amsan wayan. Tana dauka ya fara cewa........"SM, am missing you badly, ki bari inzo in ganki yau dan Allah. Karkice a'a please SM". Ya fada pleadingly.

Ajiyan zuciya taybah ta sauke sannan tace "Bari in tambaya big bro tukunna, i'll feed you back". Ta katse wayan batare data jira me zai ce ba.

Rufaida ta kalleta tace, "kici gaba kin ji, dankin samu yana son ganin ki ne kike mai wulakanci. Ki cigaba amma".

"Haba aunty rufy, nifa tsoro nake kar mijinki yamun fada". Cewar taybah.

"Ya miki fada akan me?kinga ni nayi nan in tayashi bacci, in kinga dama ki bari yazo, in kinga dama kin hanashi" ta fada tareda nufan dakin su tabar taybah a zaune a wurin.

Shiru taybah tayi a zaune, ita gayen ne ko kadan bai mata ba. Duk ya wani bi ya takura mata. Tayi tsaki a bayyane sannan tayi dailing numbern shi.
Aii kaman jira yake ringing daya ya dauka yana cewa...."Allah yasa good news zaki bani SM".

"Zaka iya zuwa bayan asr". shikenan abunda ta fada ta kashe wayarta. Daki ta wuce itama tnda dan hiran nata na islamiyyah sai anjima zai dawo.

*4:32pm*

Wayan taybah tayi qara, tana dubawa taga glue din nata ne me kira, tasan kuma cemata zaiyi ya qaraso. Sai kawai ta daga wayan tareda cewa "gani nan zuwa".

Mikeqa tayi tana gyara zaman hijab dinra wanda ya saje da baby pink atamfar jikinta. Ko arzikin kwalliya bello be samu ba tsabar ba'ayi dashi.

Seda ta leqa dakin rufaida tunda saleem ya fita ta fada mata zata fita wurin bello sannan ta wuce.

Akan wasu kujeru farere ta hangoshi zaune. Qarasawa tayi ta gaida shi, ya amsa yana qare mata kallo.

Dukda ba makeup a fuskan ta, she's still as cute and sweet asbhe can remember.

Motar faysal na hango ta cusu kai gidan. Tun be gama parking din motar ba ya hango taybah zaune da who knows who tana murmushin nan nata dayake bala'in so.

Nan da nan yaji zuciyar shi na zafi. How dare she? Shi yana can ya qasa zaunevya qasa tsaye thinking about her, amma ita tana nan tana hira da saurayinta. Does this mean she's not feeling what he is feeling?.

Damn!, runtse idanunshi yayi wani zafi na ziyartar zuciyar shi.

*©MSS MJAY*
[12/15/2016, 10:48 PM] Mss Mjay💅: WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG
*KUNDIN KADDARA*
WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

Written by
*MSS MJAY*

In dedication to
*SEMBYY LUFF*

*This chapter is for you my xoxo...thank you fpr everything, the encouragement, the support, the slaps, the winks....everytyn. I love you alot, from the beginning to the end of seven seas❣😍*

*18*

Runtse idanun shi yayi a hankali, yayin da wani zafi ya ziyarci zuciyarshi. Taybah fushi take dashi.....Noo!, that can't be, dole ya nemo mafita.

Juyawa yayi ya dubi su rufaida, wadda itama ta tsaya kallon taybah ne, yayin dashi kuma saleem yake cin abincin shi ba tare daya damu taci ko kar taci.

"Sis, taci wani abune da yamman nan?". Cewar kamal yana duban rufaida.

"Ban ganiba nikam, yarinyar da tunda ta shiga daki bata fito ba saida ta tashi daura abinci". Rufaida ta amsa.

Tsaki saleem yaja ganin yanda duk suka damu danta cr ta koshi...."ku kyaleta mana, inda tana jin yunwa da zata ci aii. Ita yarinya ce da saikun sata a gaba zata ci abinci?.....mtswwww so irritating!". Yaci gaba da cin abincin shi kaman bashi yayi magana ba.

Taybah ma da tsayuwar da isheta, wucewa daki tayi abinta.

Shiru faysal yayi ya kasa cewa komai, kallon abincin gabanshi kawai yake amma ya kasa ci.

Miqewa yayu daga table din tareda fara tafiya.
Rufaida ce tayi saurin tsayar dashi tana fadin..."baka ci abincin ba bro, ko spoon daya banga kayi ba".

Ba tare daya juyo ba yace...."I've lost my apatite sis, mayb anjima".

Taybah na kwance akan gado tana karanta sabon littafin sheldon data siyo titled "if tomorrow comes" taji wayarta na ruri,a hankali ta jawo wayar ta duba mai kiran.

"Yaa rabb!!, kaman nasan kaine me kira dama". Ta fada a bayyane sannan ta amsa wayar.
"Salamu alaika". Taybah ta fada a hankali
"Wa alaikis salaam, SM bakiyi bacci ba?. I couldn't sleep over here, been thinking about you, kinsan yanda kikayi kyau kuwa yau".

Blushing taybah ta fara, sannan ta share maganar tana cewa....."Am sorry about dazu, kayi hakuri dan Allah. I have no idea yau zezo, and i never thought he'll act that way...kayi hakuri".

Ajiyar zuciya bello ya sauke sannam yace.."in tambayeki wani abu dan Allah?".
"Sure, why not". Taybah ta amsa.

"Waye shi a wurinki?"
"Yaya na ne".

"Same mum and dad?".

"Naaah, cousin dina ne".

"Taybah, wait, lemme get this straight.... he's your cousin, and he acted that way danya ganmu tare? Bakya tunanin ko he likes you ne?".

"Lmoa😂😂😂😂😂
Am sorry zauj, dariya ka bani ne sosai. Future impossible tense kenan aii, haka nan yaa faysal yake, kullum cikin mun fada, so don't worry....am all yours❤

Ba karamin dadin maganar ta bello yaji ba, yanxu yasan ya riga ya siye zuciyar taybah.

Ita kuma a ranta cewa take.."its better na kama wanda nakeda da kyau, babu wata alama datq nuna yaa faysal zai taba sona.

Haka dai suka sha hiran su ta love, sannan aka kuma WhatsApp aka cigaba.

*2:15am*

Faysal ne keta faman juye juye ya kasa bacci, he's in love kuma baya so ya admitting yana son taybah, She's just a girl, inta raina shi fa?. Amma kuma bazai iya jurar ganinta da wani ba...meya kamata yayi? He's really lost.

Haka ya kwana yanata saqe saqe a ranshi. Da safe koda ya tashi he was restless.

Wuraren karfe 19 na safe taybah ta fito daga dakinta cikin shigar wani pakistan riga da wando deep red, tayi rolling kanta da baqin gyale tareda applying simple make-up. Ma shaa Allah, tayi kyau sosai.

A zaune a falo ta samu su rufaida, amma faysal baya cikinsu.

Rufaida ce tace...."yauwa, dama ina batun kiranki ne....tun dazu ina kiran wayan faysal yana ringing amma bai dauka ba, kamal yaje yace dakin a kulle ne. Dan Allah kije ki duba shi yazo muyi breakfast".

Badan taybah taso ba ta nufi BQ din gidan. Tun daga nesa take jiyo kamshin turaren da faysal yake using (Geo Amani) wanda take matukar so take kuma jin dadin shi.

A falo ta ganshi kwance kan three sitter, yana sanye da wando three quarter light brown da black din shirt, ya dafe kanshi kaman wanda kan nashi ke mai ciwo. Gashin kanshi a kwance yayi kyau.

Qarasowa gabanshi tayi ta tsugunna, nan da nan faysal ya bude idanunshi jin qamshin turaren taybah.

Nan kuwa yayi tozali da ita a gabanshi, looking soo cute.
Kamar daga sama ya jiyo muryarta tana cewa...."Aunty rufy tace ka fito ayi breakfast kai ake jira".

Tana gama fada mai haka tayi gaba abunta ba tare data jira mezai ce ba kuma.

*©MSS MJAY*
[12/15/2016, 10:48 PM] Mss Mjay💅🏾: WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG
*KUNDIN KADDARA*
WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

Written by
*MSS MJAY*

In dedication to
*SEMBYY LUFF*

*I dunno, and i don't have the exact words to use for someone as sweet as you MIEMIEBEE....but all thesame, i want to show my sincere appreciation and gratitude for all you did. Thank you swthrt, your motivation means alot*

*19*

Suna zaune a dinning kowa na breakfast banda faysal daya kasa cin abincin da yawa, dukda kuwa he is hungry, amma damuwan dake ranshi ta hanashi jin taste din abincin a bakin nashi.

Rufaida tana lura da yanda ya zama cool ta kuma rasa dalilin chanjawar tashi lokaci daya. Bata san cewa faysal na fama da love sickness bane😂😂😂😂

Miqewa yayi daga table din yana cewa...."sis, yau zan koma inada project din daban gama ba.....lemme go get ready".

Ba tare daya jira me zata ce ba yayi gaba abunshi. Taybah da kamal ma suka miqe suka wuce daki.

"Hubby, is something wrong with faysal ko idona ne? Dan naga kaman something is troubling him". Rufaida ta fada in a serioys tone looking concerned.

"Nima dai haka na lura, amma who knows, maybe stress ne kawai and nothing more....".

Wuraren biyu da rabi na rana faysal ya bar garin abuja da tarin damuwa a ranshi. Koda ya isa gida Ammi ma ta lura da sauyawar shi sai yace mata gajiya ce kawai tamai yawa.

*2 weeks later*

Taybah na kwance a falo ita da rufaida suna hira, ranar ta kasance ranar Thursday ce saboda haka su kadai ne a gidan.

Misalin 11 na safe wayarta ta fara ruri. Koda ta duba wayar sai taga faysal ne ke kira. A tunaninta ummu ce tunda ita take kiran ta da wayan shi sometimes. Sai kuma ta tuna yau school day ne aii, amma dai mayb wani abu ne ya hanata zuwa.

"Ma little princess, kin tashi lafiya?". Har cikin brain dinshi faysal yaji sautin muryarta, yayi shiru kamar bazai yi magana ba saboda yadda dadin muryan ya ratsa zuciyar shi.

A hankali kaman mai ciwo baki yace..."Admission dinki ya fito, an baki sociology, ki shirya anjima zan shigo in daukeki, dad nason ganinki".
Da sauri y kashe wayar dan baya son ya qara jin muryar tata balle hankalin shi ya qara tashi.

Wani ihu taybah tasa har taba rufaida tsoro, da gudu taje ta rungumeta tana cewa na zama yar jami'a sister, admission dina ya fito".

"Maa shaa Allah! Congrats swthrt, wani course?". Rufaida ta tambaya happily.

"Sociology, zanje in shirya kayana, jos tayiiii kiraaaaa". Ta fada haka cikin murna tarefa nufar dakin nata da gudu.

Da sauri tayi dialing din numbern bello, ringing biyu ya dauka yana fadin....."kaman kinsan am missing you deadly down here".......... Taybah cikin murna tace...."SM admission dina ya fito....zan zama sociologist!".

"Alhamdulillah, this calls for a celebration durl, congrats. Allah ya nunamun ranar dazan raka ki alter ki karba degree dinki".

"Awwnnn! see you, tunban faraba har ka fara maganan karban cert, abeg je kayi aiki, zan tafi jos gobe".

"Then i have to come see you kafin ki tafi".

Da sauri taybah tace...."A'a ka bari inna dawo ran sunday kaxo.....pleaseeeee" ta fada in a manner data san yana so.
"Fine, naji. Allah ya kaimu.

Haka dai suka cigaba da hirar su cikin nishadi.

Da yamma kuwa saiga faysal ya iso, taybah yau farin ciki kawai take, ga admission, gashi zataje taga mammy dasu yasmin.

Faysal ya lura da farin cikin da take ciki, he couldn't help but be happy shima, she's happy, shima dole yaji dadi aii.

Washegari kuwa around 10am suka dauki hanyar jos. Basuyi wani nisa da fara tafiya ba wayar taybah ta fara ruri, gashi ita ta fara bacci, cuz saboda murna jiya ko baccin kirki batayi ba.
Wayar na ajiye akan laps dinta ne, kawai sai faysal yasa hannu ya dauki wayar yana duba mai kira.
"My Sm" shine abunda ya gani a rubuce a wayar tata.
Badai gayen ranar bane soulmate din nata😳

Aii baisan lokacin daya taka wani wawan birki ba, nan da nan taybah ta tashi daga baccin da takeyi.

Gangarawa yayi gefen titin sannan yayi parking din motar tareda daura kanshi akan motar zuciyarshi na boiling.

*©MSS MJAY*
[12/15/2016, 10:48 PM] Mss Mjay💅: WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG
*KUNDIN KADDARA*
WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

Written by
*MSS MJAY*

In dedication to
*SEMBYY LUFF*

*20*

A rufe idanun nashi suke har yanxu, yayin da taybah ta takure a tata kujerar cikin tsoro, batasan meya faru har haka ta kasance ba.

Kamar daga sama wayar tata ya qara yin ruri, amma saita tsinkayo rurin wayar a wurin faysal....toh ya akayi wayata taje wurin shi?.

Haka aka ta kiran wayar nata, faysal bai dago ba balle ya bata wayar taga mai kira, shi kuma bai dauki kiran ba.

Sun kai kimanin 30mins a zaune a wurin kafin daga bisani ya dago kanshi da yayi jawur saboda bacin rai ya kalli taybah. Bece komai ba ya tada motar suka cigaba da tafiyar su.

Around 1:23 suka isa jos. Kwanakin da taybah tayi jos, tayi sune cikin farin ciki, taga mammyn ta dasu yasmin kuma yanxu Alhamdulillah akwai improvement a halayyar baba ta rashin kula da al'amuran su.
Taje wurin hafsah suka sha hira......gashi kullum tana tare da princess dinta suna hira, girki ko karatu. Kwanakin biyu dai ba shakka tayi su cikin annushuwa.

Yayinda a bangaren faysal everything seems to have turned upside down, gashi dai ga taybah kullum a gida daya, amma instead of ya samu sauqin tunaninta....a'a, sai ma qaruwa da tunanin nata yayi a ranshi....seeing her talk, smile, eat, walk...everything about her drives him crazy!...

Ran monday kuwa da sassafe faysal ya tafi mayar da taybah abj, ya tayata registration before ya kuma.

Sun isa da wuri, sai kawai suka wuce school direct dan su fara tunda shi yanada aiki dayawa daya baro a office.

*3 weeks later*

Su taybah an zama university student....ta hadu da new friends who are fun to be with... Asma'u and saratu😊

Yau sunday, tana kwance falo tana karatu, yayin da suke hira da rufaida jefi-jefi.,...wayarta dake kan center table ya fara ringing.

Tun kafin ta duba rufaida ta fara dariya tana cewa....."Ni nasan bawanda ke kiranki banda your glue, kuma yanxu dan bakida kunya a gabana kike waya dashi".
Dariya taybah tayi tareda dauko wayar, tana dubawa kuwa taga shidin ne yake kira..... Ta dauki wayar tareda sallama....ya amsa sannan yace...."kin wuni lfya?.
"Lfya qlw"
"Taybah....tell me dan Allah, dan Allah ki gayamun if i mean nothing to you in sani, tun yaushe nake binki ki bari inxo in ganki kinki...why? Nace in biyoki school kin ce noo...inzo gida ma nooo.....haba taybah ya kike so inyi ne? You think video call solves everything ne? Ki gayamun what yoy have in mind a kaina lemme know my stands!"

Shiru taybah tayi, tasan yau kam ta riga ta qure hakurin shi, gashi yaa faysal yana gari tun jiya, amma yau kam, she'll have to let him come over, yana hakuri da ita aii.
A hankali tace mai...."if you are not busy, zaka iya zuwa".

"SM, dagaske kikeyi dan Allah, you mean i should come over yau, thank you swthrt, a shirye nake yanxu zaki ganni a gidanku". Ya katse wayar.

Taybah ta dago ta kalli rufaida a sanyaye....rufaida tayi murmushi sannan tace....."ki tashi kije ki shirya, worry less about faysal, zan mishi magana".

"A'a ki barshi kawai, inna shirya zan sameshi a garden din da kaina in fada mishi". Cewar taybah tana dosan dakin ta.

*30 minutes later*

Around 4:34pm kenan lokacin, faysal na zaune a garden yana aikin daya zame mai farilla yanxu kullum wato tunanin taybah.
Kaman daga sama yajiyo kamshin turarenta na oud na tashi, yana juyowa kuwa ya hango ta sanye da wata bahrain gown peach colour, tayi rolling black veil, ga fuskan ta dauki make-up daidai gwargwado.

Sake baki kawai yayi yana kallonta, ko kifta idanun shi ya kasa harta karaso gabanshi ta tsugunnan.

Tsoro ta kama taybah dan bata manta marin data sha ba months back, kar azo a maimaita irin na ranar.

Daurewa tayo with confidence batare data dago kanata ba ta fara magana....."yaa faysal, dan Allah kayi hakuri, bello ne yakeson zuwa kullum saiya dameni shine nace dan Allah kayi hakuri ka bari yaxo yau".

Dammit!!!....wato duk wannan kwalliyan shi tama kenan?. Taybah naso ta kashe shi knn.

Idanun shi suka kada sukayi jawur dasu saboda bacin rai....kamar daga sama taybah tajishi yana cewa........."Taybah, ko kike ki kasheni koh? Taybah look into my eyes and tell me you don't know the hell am going thru saboda ke....i showed you signs, nayi iya qoqarina in nuna miki you just don't seem to care the hell am going thru!. Ya fada a tsawace kamar zai daketa.

*©MSS MJAY*
[12/15/2016, 10:48 PM] Mss Mjay💅🏽: WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG
*KUNDIN KADDARA*
WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

Written by
*MSS MJAY*

In dedication to
*SEMBYY LUFF*

*21*

"Taybah!, look into my eyes, kalli cikin idanuna kiga the pain am going through for you, can't you see that!?. Ya fada a tsawace yana girgiza ta.

Taybah sandarewa kawai tayi a wurin, ta kasa cewa komai, karfin jijigawar daya mata ne yasata fashe mai da kuka....."What's wrong with you yaa faysal? Me kake nufi da furucinka?...... Ka sakeni!!!, don't you dare, dont you dare lay your filthy hands on me again!. Ta fada tana yin baya baya.

Nana da nan jikin faysal yayi sanyi, badai taybah ta tsaneshi haka ba, if that is the case, then yana cikin matsala.
Sulalewa yayi ya durqusa a gabanta

"Taybah, kalleni please, bakiga yanda na koma bane? Bana jos bana abj.....bana concentrating akan aikin gabana. Kullum cikin tunaninki nake. Look into my eyes and tell me bakida koda slightest feeling ne for me". Ya fada muryarshi na rawa.

Juyawa taybah yayi da gudu tabarshi a gurin a tsugunne.....ko ganin gabanta dakyau batayi saboda kukan data keyi.

Daidai lokacin shikuma bello ya gama parking din motarshi a cikin gidan. Hango taybah da yayi tana kuka hade da gudu yasa shi ya fito daga motar, ko kulleta beyi ba ya nufeta cikin sauri.

Ganin mutum kawai tayi a gabanta a tsaye, tana dago idanunta ta saukesu akan bello. Nan da nan taji wani haushi ya turniqe ta, rana ta farko data fara jin ta tsane shi kenan. Dukda dama can ba sonshi take ba.

"SM, Ifya dai koh?". Bello ya fada cikin damuwa.

"Malam, find your way out of this house tun kafin ranka ya baci, kai wane irin nataccen mutum ne?".

Cikin mamaki taybah ta juya tana kallon faysal dake faman huci kaman zaki😹😹😹

Murmushi kawai bello yayi, if he's not mistaken.... Wannan cousin din na taybah is inlove with her without doubt.

Inko haka ne, akwai matsala dan shikam baijin zai iya kyale mishi taybah. Taybah shi take so, not her so called cousin.

"Haba yayanmu, na riga na zama sirikin ka fa....let bygones be bygones". Cewar bello cikin raha.

Faysal yaji kaman ya zuba mishi ruwan zafi a zuciyarshi.....bai yi wata wata ba ya kwashe bello da mari har biyu.

Ba karamin firgita taybah tayi ba with his action....mari? Yau kuma marin kan bello ya kuma.

"Waya baka ita? Nace waya baka ita?? Kai har kanada guts din gayamun wai kai siriki na ne...yaushe hakan ya faru?......my friend will you get out of my sight before i loose my patience". Faysal ya fada a harzuqe.

Bello dahar yanxu hannunshi ke dafe da kuncin shi yayi shiru kawai yana kallon ikon Allah, mari?? Yau shi wani ya mara akan mace??. For a moment he was thinking ko shima ya rama marin, Amma kuma yaci darajar son dayakema taybah, if not yau daba abunda zai hanasu dakuwa da juna.

"SM, i love you alot, nasan kinsan haka....kinji yanda zuciyata ke zafi kuwa saboda kukan nan da kikeyi? Please ki share hawayen nan.....ki barsu sai randa za'a kaiki gidana......then you can shed the tears of happiness. I love you and take care of yourself for me".

Yana gama fadin haka ya juya ya nufi motar shi tareda tafiya.

Taybah ta juyo cikin haushi ta kalli faysal da idanunta, kallon tuhuma da rashin jin dadin abunda ya aikata.

"Don't look at me that way dan Allah, ba laifina bane". Faysal ya fada pleadingly.

"Kwarai kuwa yaa faysal, ba laifinka bane, laifina ne dana kasa nuna maka matsayin bello a wurina ba, wannan marin daka mishi bashi zai hanashi kulani ba, ba ka shi zai hana ni in kulashi ba. Kuma ka sani ni kayi disgracing a idanun shi ba kowa ba".

Tana gama fadin haka ta juyada gudu ta nufi cikin gida.

"T...tay...taybah, tsaya kiji, please ki tsaya. Don't do this, i love you". Ya fada yana dafe kanshi dake barazanar ciwo kaman ya cire.
"Yaa rabb!!, what have i done?.

*monday morning*

Taybah ta fito cikin shirinta na zuwa makaranta, sanye cikin material lemon green wanda akama dinki riga da skirt da suka matukar mata kyau.

Dining ta nufa dan kowa ya hallara ita kawai ake jira.
Faysal da tun fitowarta yake kallonta saboda kyan data mishi.

"Whoa!, Aunty taybah, kinga yanda kikayi kyau kuwa?. I have the most beautiful aunty in the world". Kamal yayi exclaiming giving her a very big hug.

Rufaida ta musu dariya tana cewa......"kajimun yaro, waishi har yasan abu mai kyau".

Saleem ya tabe baki sannan yace..."ina yasn kyau kuwa yana kiran wannan mai kamada laujen beautiful, ni am starving, ko kiyi serving dina ko in tashi inyi kinga na kusa inyi latti". Ya fada in a serious tone.

Faysal dai bai ce komai ba har aka gama breakfast din. Taybah da kamal sukayi gaba abunsu.

*11:40am*

Rufaida ta samu faysal a dakin shi dake BQ kwance, yayi zurfi cikin tunani har baisan lokacin data shigo ba. Saida ta taba kafarshi sannan ta dago yana kallonta........"sis maman biyu, kece da kanki".

Ya fada teasingly ganin yanda take kallonshi ba wasa a fuskan ta.

""Faysal, who am i to you?". Rufaida ta tambayeshi seriously

"A sistet i adore and love alot".

"Good, now tell me, mene damuwarka ne? This dayz you are soo cool, kullum cikin tunani ko abincin kirki na lura baka son ci sosai......me yake damunka ne?. Rufaida ta tambayeshi.

Sunkuyar da kai faysal yayi, ya fada mata damuwarshi ko yayi shiru, Amma it will be better inya bari sun daidaita da taybah before he can vouce it out to anyone.

*©MSS MJAY*
[12/15/2016, 10:48 PM] Mss Mjay💅: WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG
*KUNDIN KADDARA*
WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

Written by
*MSS MJAY*

In dedication to
*SEMBYY LUFF*

*22*

"Sister, please koma mene yake damuna you'll know when the right time comes...for now ki manta kawai".

Rufaida tayi shiru tana kallonshi, koma mene ke damun faysal, its serious.

"Shyknn bro, zanci gaba da tayaka addu'a....Allah tabbatar da mafi alkhairi".

Yammacin ranar taybah na zaune ka darduma a garden riqe da hand out tana karatu.

Alal haqiqa ba karatun take ba, tayi zurfi ne cikin tunanin maganganun da faysal ya gaya mata jiya. Yea, itama tasan deep inside akwai wani weird feeling da take feeling for him, she can't say what that feeling is truly is or what's all about.

Kamar daga sama tajiyo kamshin turarenshi mai kashe mata jiki,wanda kuma take matuqar so. Kafin tayi yunqurin yin komai faysal ya tsugunna a gabanta. Kallonta kawai ya tsaya yi...how beautiful she is just being natural....she's an angel..yet she drives him craxy!.
Shirin da taybah taji yayi yawa ne ya sata dago kanta a hankali....caraf suka hada idanu. A yau sai taybah ta samu kanta da kasa dauke kanta daga kallon faysal....yea, she can see the pain, the love deep inside his eyes.
Sunkai kimanin 15mins sitting there, just staring at each other....kowa kuma da abunda yake sani akan danuwan shi.

A hankali taybah ta dauke fuskan ta daga kallon da suke ma juna......faysal yayi saurin cewa..."Noo taybah, look at me please, look into my eyes and tell me har yanxu bakiga the pain am going thru ba....mena miki bakya sona taybah, ko tausayina bakya yi?... Kullum cikin tunani nake, ga aiki a gabana na kasa nitsuwa inyi....what do you want me to do pretty face? Tell me".

"Yaa faysal, give me time please, i need to think this thru".

"Think thru? Think thru wat taybah....kinga if you hate me ki gayamun kawai in sani...kinsan sleepless night nawa nayi? Kinsan yanda nakeji cikin raina sbda son danake miki?....Noo! Duk baki sani ba bcuz thatz not the way you feel".

"Yaa faysal mana!, i'll give you my answer in a week time".

"Nah, in a week mayb na tsufa a asibiti...make it tomorrow!. Abunda kawai yace kenan ya tashi yabar garden din dafe da kanshi dake barazanar fashewa sbda ciwo.

*9:23pm*

"Am confused gaba daya hafsah, na rasa yanda zanyi". Taybah ta fada in a sad tone riqe da waya a kunnen ta.

"Listen taybah, kibi abunda ranki yakeso, kin riga kin admitting faysal kikeso, wani dogon tunani ba naki bane. Tell me the use of soyayyah shi yana yi ke bakya yi?...tunda kinada wanda kikeso yake kuma sonki fine, go to him with open arms". Hafsah takai karshen dogon sharhin ta.

Ajiyar zuciya taybah tayi bayan sunyi sallama da juna. yea, its time she decides about her

future!.

Washegari taybah na gama hada breakfast ta kuma bacci, dan yau batada lectures sai 12.

Misalin 10:36 ta fito daga dakinta sanye da bakin wando daya kamata da top ja, saita daura bakin dankwali a kan nata yayin da dogon gashinta yayi kwance a gadon bayan ta.

Rufaida ce zaune a falo tana cin apple, taybah na ganin haka ta kwashe da dariya tana fadin....."Allah bar mana ke mana biyu..ci fruits da kyau mu samu healthy babies... Wooo...harna ganni rungume dasu...soo cute". Taybah ta fada tana zama kusa da rufaida akan three sitter.

Duka taybah ta zuba mata a baya sannan tace.."kiga twins a womb dinki muguwa...kiwa Allah ki rabani da maganar twins dinnan".

"Ai sai kin haifesu.....shi wannan doctor hubbyn naki ya miki scanning musan me muke ciki yaqi.....mijin nan naki akwai riqaqqen akida".

"Laaa, yanxu dan bakida kunya a gabana kike zagin mijina, kedai bari taybah, kiyi fatan samun miji irinshi....he's loving, handsome, caring, ga iya love.....nikam anya akwai masoyi irin doctor hubbyna kuwa". Rufaida ta fada tana runtse ido tareda daura hannunta akan kirjin ta irin tana feeling love vibe..lol..

"Na shiga darii.....aunty rufy kinyi nisa, yanxu banda kissing din juna da kuke a gabana yau har wani fannin kika tabo?. To nikam nayi nan..yunwa nakeji". Cewar taybah tana nufan dining.

"Nayi daki in kwanta, inkin tashi zuwa lectures kimun magana". Rufaida ta fada sannan ta nufi dakinta.

A nutse taybah take breakfast dinta..fish pizza tayi da cottage pie, sai madarar waken suya datayi.

Ta gama breakfast kenan ta nufi hanyar dakinta taji muryar faysal yana cewa...."Good morning pretty face, Allah yasa kin gama tunanin naki".

Juyowa tayi a hankali ta kalleshi, yana sanye da baqin wando shima da jan top....laaa, anko sukayi knn.
Dago ido tayi ta kalleshi taga ba abunda yake banda aikin kallonta.. Sai a sannan ta tuna kayan jikinta.

Da gudu ta juya ta nufi dakinta, saida ta kama handle din kofan zata bude sannan ta juyo a hankali tace....."I LOVE YOU YAA FAYSAL". Ta fada tareda fadawa dakinta ta kulle zuciyarta na

bugawa.

*©MSS MJAY*
[12/15/2016, 10:48 PM] Mss Mjay💅🏽: WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG
*KUNDIN KADDARA*
WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

Written by
*MSS MJAY*

In dedication to
*SEMBYY LUFF*

*This chapter is for you my xoxo...am soo proud of you, you made it and ended your story in a UNIQUE AND ENTICING manner...THE CHARMING WAS ONE OF THE BEST BOOKS I'VE EVER COME ACROSS....am so ao proud of you. Allah qara basirah in loads. I love you to the moon, round and back❤*

*23*

Jingina da kofan taybah tayi zuciyarta na bugawa da sauri da sauri. Dafe saitin zuciyarta tayi tana murmushi, ashe dai xata iya bayyanah her feelings to him.

Faysal daya sandare a wurin ko motsi ya kasa yi, she left him speechless tsaye a wurin yana mamakin ta. Baisan lokacin da wani murmushin farin ciki ya subuce mai ba.

Misalin 11:15 taybah ya fito cikin shirin atampa purple riga da skirt, tasa purple hijab dinta ga

make up dinta dan das a fuskan ta.

Tana bude kofar dakinta ta hango faysal zaune kan three sittern dake saitin dakinta.
Daskarewa tayi a wurin saboda batayi tunanin ganin shi a wurin ba. Harta juya da nufin komawa daki domin yanxu wata matsanan ciyar kunyan shi ne ke damunta.

Da sauri faysal ya tsayar da ita yana fadin...."pretty face, ina zaki kuma? Come back here dan Allah and lemme have the pleasure of taking you to school today".

Rufe fuskanta tayi da hannunta tana murmushi. Sannan a nutse ta nufi dakin rufaida, koda ta shiga ta samu rufaida na bacci hankalinta kwance. Sai kawai taybah ta fita tareda rufe mata kofan dakin ta nufi waje.

A harabar gidan ta hango faysal tsaye a gaban motar shi, yana hangota ya tashi da sauri ya bude mata gidan gaba. Wata kunya ta rufe taybah amma kuma she's happy beyond words na yanda yake showing his care akanta.

A hankali yake driving din, yanayi yana kallonta, sometimes su hada ido su sake ma juna murmushi...sometimes kuma shi kadai yake kidanshi da rawar shi.

A hankali ya tsinkayo muryarta mai matuqar zaki tana cewa...."yaa faysal, ya kamata ka koma jos hakanan, concentrate on your work yanxu please.... Am all yours". Ta fada tana rufe fuskanta.

Murmushi yayi cikin farin ciki, yau yana cikin farin ciki marar misaltuwa....yea, taybah tashi ce. Wani zafi yaji ya ziyarci zuciyarshi sakamakon tunawa da bello da yayi.
"Noo pretty face, ba gaskiya bane....in har abunda kika fada gaskiya toh ki kira that so called boyfriend din naki a gabana and end things". Ya fada yana wani shan toka.

"Kaima kasan haka bazai yiwu ba, a hankali zanbi da bello, ba yanda za'ayi lokaci daya in kirashi in cemai am no more interested.... Thatz not possible yaa faysal".

"Not possible kamn ya? Kinfi son happiness dinshi akan nawa kenan?" Ya tambaya yana kallonta.

Dagowa tayi da sauri ta kalleshi, idanunta sun ciko da kwalla

"Yea, kinfi son happiness dinshi akan nawa. Am the jealous type pretty face, ni am very jealous akan abunda nake so and believe me i don't wanna share you". Daidai lokacin yayi parking a gaban faculty dinsu.

"Kaidai yaa faysal ka cika rigima kaman karamin baby......awww na manta you are my baby ashe". Ta fada tana kashe mai idanu.

Aii nan da nan mr.faysal ya manta da fadan da yakeyi. Taybah ta kama murfin motan da nufin budewa ta tafi, sai taji ansa lock.

"Ki tsaya muyi sallama mana, thought kince kin gaji dani, ina komawa gida xan hada jakata in koma".

"Awwnn yaa faysal...am gonna miss you, ka kula da kanka for me dan Allah.... Karfa kaje kana kallonta wasu yanmatan fa". Taybah ta fada cikin shagwaba tana turo those sweet lips of hers.

Mutuwar zaune kawai faysal yayi yana kallonta. Admiring every single thing about her.

🎈🎈WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

Kwanci tashi babu wuya a gurin Allah, gashi har soyayyah mai karfi ta shiga tsakanin taybah da faysal. Domin ni kaina shedah ce akan irin soyayyar da sukema juna.

Duk wainar nan da ake toyawa rufaida bata taba lura ba, balle uban gayyar doctor saleem wanda jininsu ko kadan bai hadu da juna ba shida taybah.

Yau taybah ta rubuta final paper dinta...an gama first semester exams. Tana fitowa ta kira faysal....."yaa faysal..ka tayani murna, yau am gonna sleep like a baby". Taybah ta fada cikin farin ciki.

"Ooo Allah ni faysal naga ta kaina, nayi nayi ki chanja mun suna kinqi ko pretty face, anyway kice kawai yau am a baby, dan nasan you gonna kill me with love". Ya fada soo sweetly.

Murmushi taybah tayi sannan tace..."kwarai kuwa mine...harsai kace inyi hakuri in barka hakanan, bye take care of yourself am gonna miss you". Ta fada sannan ta kashe wayar.

Tana isa gida ta nufi ciki da sauri tana fadin "aunty rufy, maman biyu kina ina? Gani na dawo kizo kimun massage".

Shiru taji ba alamun rufaida sai kawai ta doshi dakin rufaidan dan gannin ko bacci take.

A duqe ta sameta tana riqe da cikin ta sai salati takeyi cikin zafin ciwo.

Zubar da kayan hannunta tayi sanna ta nufeta cikin sauri.

*©MSS MJAY*
[12/17/2016, 5:55 AM] Mss Mjay💅: WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG
*KUNDIN KADDARA*
WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

Written by
*MSS MJAY*

In dedication to
*SEMBYY LUFF*

*25*

A razane su duka biyun suka dago suka dubi dad.........T...Ta....Taybah fah kace dad". Saleem ya fada in shock yana zare ido.

Taybah kai kawai take girgizawa tama kasa cewa komai, nan da nan hawaye suka fara zuba kamar famfo.

"Kwarai da gaske, ita nace saleem in kuma baka so ka fada kar kaji komai i understand stuffs like this". Dad ya fada.

Shi waye da dad zai mai kyauta yaqi karba, ai da kunya ma inya ce bazai karba wannan kyautar da aka mai ba. Taya zai dubi idon dad ya fada mai bayason niece dinshi....naah thatz not possible.........."Na yadda na amince dad, nasan su Alhaji basuda matsala, zanje musu da maganar yanxu inna koma gida". Saleem ya fada murya na rawa saboda bacin rai.

Duk kokari taybah nata hana kukan dayake son kufce mata ta kasa, nan da nan wani kuka mai

ciwo ya kucce mata......bata jira me za'a kara cewa ba ta tashi ta nufi dakinta da gudu. Faysal wanda ke shigowa gidan lokacin ya hango sanda take shiga dakin nata da alama kuma kuka take.

Ganin su dad zaune a parlor dinne ya hanashi binta yaji abunda ya faru. Gaida iyayyen nashi yayi sannan suka gaisa da saleem.

"Nagode saleem, ka nuna mun cewa inada iko a kanka, Allah ya maka albarka ya albarkaci rayuwar kamal....zan kira Alhaji da kaina mu tattauna...tashi ka tafi". Faysal dai yayi zaune ne a wurin kaman gunki ya kasa cewa komai, wa kuma za'a aura mai?.

Saleem ya isa gidansu cikin mawuyacin hali, ko gabanshi baya gani da kyau ya qarasa shiga cikin gidan. Hajiya sadiya mahaifiyar shi na zaune a kan kujera da hisnul muslim a hannunta tana karantawa.

Sallamar dan nata data jine da kuma yanayin data hango shi yasa ta ajiye littafin gefe sannan ta bishi da idanu bayan ya kwantar da kashi a gefen cinyanta tareda runtse ido. Ba tare data ce komai ba ta fara sha lallausan gashin dake kwance a kanshi sannan a hankali ta fara karanto mai suratur rahman.

A hankali yanayin da yake ciki na tsantsan bacin rai ya fara gushewa har ya koma suna karatun tare, saida suka kai karshen surar sannan suka shafa addu'oin da sukayi.

"Auta, zaka iya magana yanxu". Hajiya sadiya tayi tambayar cikin kulawa.

"Wai daddyn rufaida ya bani niece dinshi in aura, Taybah dake zaune tareda mu a abuja". Ya qarasa maganae kwalla na fitowa daga idonshi.

Hajiya sadiya ta lura dan nata baiyi na'am da auren ba, amma aii da kunya Alhaji usman ya musu kyauta suqi karba.
"Inaso ka gane wani abu auta, ita rayuwar nan daka gani kowa da nashi KADDARAR, a KUNDIN kowa an rubuta mai irin tashi KADDARAR, fatan mu kawai shine Allah ya dora mana KADDARAR da zamu iya dauka. A naka KUNDIN an riga an rubuta cewa zaka rasa rufaida sannan ka auri taybah, addu'a kawai zamu tayaka da ita, Allah ya baka farin cikin zama da taybah fiyeda yanda kaji dadin zama da rufaida". Hajiya sadiya ta qarasa dogon sharhinta tana goge kwallar data taru mata.

Rungume mahaifiyar tashi yayi sosai yana kuka mai han tausayi, sai yau ya qarajin dacin rabuwa da rufaida, she was the best, infact perfect to him.

Saleem ne kawai da namiji a gidansu, yanada yayu mata har guda hudu, samyrah, kausar,

iklimah da khadeejah.

🎈🎈🎈🎈🎈WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

Taybah tunda ta shiga daki ba abunda take banda kuka, kuka kuwa mai tsanani, shyknn yanxu burin auren da suja ci itada faysal ya rushe, yanxu duk soyayyar da sukema juna ta tashi a banza. Ya ilahi! Wannan wacce irin KADDARA ce ta hau kanta.
Wayarta dake gefenta a ajiye ta fara ruri, tana dubawa kuwa taga faysal ne yake kira. Nan da nan wani kuka mai ciwo ya qara zuwa mata, in komai ya daidaita wani sati ta zama matar saleem kenan. Tana cikin tunanin ne taji message ya shigo wayarta........" Ki sameni a BQ dan Allah, ina jiranki".

Tun daga nesa ta hango shi a tsaya ya juya bayanshi yana saqale da hannuwanshi ta baya...qarasawa tayi a hankali sannan tace...."yaa faysal, gani".

She was shocked at what she was seeing,hawaye ne kwance shabe shabe a fuskarshi, idanunshi sunyi jawur saboda bacin rai da tashin hankalin dayake ciki.

*©MSS MJAY*
[12/17/2016, 5:55 AM] Mss Mjay💅🏾: WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG
*KUNDIN KADDARA*
WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

Written by
*MSS MJAY*

In dedication to
*SEMBYY LUFF*

*24*

Dago rufaida tayi cikin tsananin kidima. Hango jini tayi yana zuba daga jikinta kaman pampo.

A gigice taybah ta dauko wayarta tayi dialing din numbern saleem.
"Yaa saleem, aun...aunty rufaida na bleeding". Ta fada muryarta na rawa.

"What?....ki tsaya gani nan zuwa gidan". Ya fada a rikice.

Ko mintuna goma musu kyau ba'ayi ba taji motar saleen ta qaraso gidan. Saleem wanda yake a gigice ya nufi cikin dakin tareda dauko rufaida suka nufi asibiti.

Emergency ward aka nufa da ita saboda yanda take bleeding, shi saleem tsabar kidima yama kasa tsayawa ya duba ta da kanshi.

*2hrs later*

Dr. Sameer ameer ne ya fito cikin sauri daga ganinshi hankalinshi a tashe yake. Taybah dake zaune sai rusa kuka take ta qasa shiru tunda aka shiga da rufaida labour room.

"Ina mijin nata yake?" Dr sameer ya tambaya.
"Gani nan doctor". Saleem ya fada a hanzarce.

"To my office". Ya fada tareda nufanoffice dinshi. Taybah ko gayyatar ta ba'ayi ba amma saida tabi bayansu.

"Kowa da irin kaddarar shi a rayuwa, khairan aw sharran...kuma kowacce kaddara da dalilinta...a kullum addu'ar mu Allah ya daura mana kaddarar da zamu iya dauka.....sai kunyi hakuri da abunda nake shirin fada muku". Dr sameer ya fada idanun shi sun ciko da kwalla.

"Dr, dan Allah ka fada mun meya faru? Tell me what the hell is wrong". Saleem ya fada impatiently.

"Am sorry to say, matarka ta haifi twins duka mata, kuma Alhamdulillah they are healthy.... Amma...". Sai kuma yayi shiru.

"Amma kuma me doctor? Ka fada mun menene matsalar dan Allah". Saleem ya fada yana hawaye.

"Kayi hakuri doctor, kayi hakuri, Allah ya baka jurar rashinta.....amma munyo iyakar qoqarin mu we couldn't save the mum".

Sandarewa saleem yayi a zaune a wurin yayin da taybah ta sulale a wurin tana salati.

Rufaida is gone? Rufaidar shi ake nufi ko wata? Noooo!!! It can't be, rufaida bazata tafi ta barshi ba. Girgiza kai kawai saleem yake kaman qadangare ba tare daya samu damar cewa komai ba.

*RIP RUFAIDA*😫😫😭😭

*43 days later*

Mutuwar rufaida ta taba kowa mussam man ma da bayan rasuwarta da kwana biyu twins dinta suma suka bita😭😭😭😭

Saleem ya chanxa, duk ya zama abin tausayi, gaskiya ne, yayi rashin mata dan rufaida mata ce tagari wadda yake alfahari da ita kuma a ko yaushe.

A bangaren taybah ma haka abun yake....zaman watanni takwas da tayi da rufaida ta koyi abubuwa da yawa dangane da rayuwa. She has lost a sister and a friend.

A takaice dai both tje two families, na rufaida dana saleem kowa mutuwar ta gigita shi.

A yammacin ranar asabar dad ya kira saleem gida da misalin karfe biyar. Falonshi ya kaishi daga shi dad, sai Ammi, taybah da saleem din a zaune.

Gyaran murya dad yayi sannan a hankali ya fara magana......."Ina qara ma kowannen mu ta'aziyar rashin ya, mata, yaruwa da duk mukayi. Allah ya bamu juriya da hakurin rashinta ya kuma haskaka kabarinta. Ba komai bane yasa na taraku a wurin nan face dan in isar muku da wata shawara dana yanke".

"Kai saleem" dad ya fada yana mauda kallonshi da hankalinshi gaba daya a kanshi...
......"Ina sonka, kuma yanda faysal yake da a wurina haka kaima kake da a wurina, na yaba da hallayar ka da kuma karamcin ka...saboda wannan dalilin yasa na yanke hukunci, amma sai in

ka yadda ka kuma amince, kar kaji kunyar fada mun in hukuncin dana yanke bai maka ba domin ni tsakani da Allah nake sonka. Saboda haka....in har ka yadda kaji kana so kaje kayo shawara dasu alhaji nan da wani sati inka amince zan daura maka aure da TAYBAH!."

*©MSS MJAY*
[12/17/2016, 5:55 AM] Mss Mjay💅🏽: WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG
*KUNDIN KADDARA*
WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

Written by
*MSS MJAY*

In dedication to
*SEMBYY LUFF*

*This chapter is for you MOMMA, wallahi i lack the perfect words to show you what you mean to me. But i love you alot....to the moon...the sun round and back❤*

*26*

Tsayawa sukayi suna kallon juna kawai ba tare dasun furta komai ba. Taybah ita kallon shi kawai take, wondering ko me yasa shi zama haka, looking soo depressed and hurt.

"Taybah, what is this i heard? Wane irin magana naji wai saleem zaki aura? Taybah how can you do this to me...kinsan yanda nake sonki kuwa? Do you know the sleepless night i went

through before in sameki?. Dan Allah kiji tausayina kije ki fada ma dad ya janye....taybah pleaseeeeee". Faysal ya fada hawaye na zubowa daga idonshi.

Taybah ma wani kuka ne yazo mata, this is the worst day of her life...zata rasa faysal dinta, rasawa ta har abada....amma wacce ita taje ta cema dad bazata aure zabin shi ba...no thats not possible.

"Yaa faysal, dan Allah kayi haquri, ya kakeso inyi ni? Taya kake tunanin zan dubi idon dad ince banason zabin daya mun?. Muyi haquri kawai mu karbi KADDARAR da Allah ya dora mana. Kayi haquri dan Allah, nikam na riga na huqura".

"I knew it! Ni dama nasan ni kadai nake haukan sonki you never seem to care about how i feel...ki fadamun kawai cewa you never loved me...say it taybah". Faysal ya fada cikin bacin rai yana girgiza taybah kaman zai balla mata kafada......."Stop it yaa faysal! You're hurting me". Taybah ta fada cikin kuka.

"Aii gwara inyi hurting dinki...the pain kike feeling yanxu ko rabin wanda nake feeling bakya ji. Haba ni nayi mamaki haka kawai dad yace yaba saleem ke, ashe ke kika je kika ce ya hada ku....ashe baki taba sona ba!". Ya fada a tsawace.

"Yes! Ban taba son naka ba kuma bazan taba son naka ba! I hate you, i hate you more than anything i've eva loved....karka qara gani nan kamun magana domin yanxu na riga da zama rabon wani". Cewar taybah cikin tsananin kuka sannan ta kwace kanta ta nufi gida da gudu........"Noo taybah, karya kike...ni kike so, you are just saying this to hurt me. Ta...tay...taybah ki dawo, tell dad ni kike so dan Allah". Ya durkushe a wurin yana kuka(nima nida momma muna tayashi😭😭😭😭

🎈🎈WWW.HAUSAEBOOKS.COM.NG

Washegari taybah ta tashi idanunta sunyi luhu luhu saboda kukan data sha jiya da daddare. Ko wayar ta taqi kunnawa tunda faysal ya dinga damunta da kira. Yanzu ma tana kwance tayi zurfi cikin tunani har bata san lokacin da ummu da kamal suka shigo dakin nata ba, sai ji kawai tayi suna cewa...."Aunty taybah, dad na kira".

A zaune ta samu dad shida ammi a parlor, durqusawa tayi ta gaida su sannan ta nema guri ta zauna.

"Taybah, bakida lfya ne?. Ammi ta tambaya........"lfyata qlw ammi".

"Kodai hukuncin dana yanke ne be miki ba? Tell me taybah in har bakya son saleem zan kira shi a fasa maganar". Dad ya fada cikin kulawa.......da sauri taybah tace"A'a dad, ba haka bane kawai banajin dadin jikina ne".

"Toh shyknn ki shirya anjima saleem nanan zuwa ku gana da juna". Cewar dad. Wani daci ya xiyarci zuciyar faysal dake tsaye bakin kofan tun daxu. Lallai da gaske taybah take data ce bata sonshi, inba haka ba ga dama dad ya bata amma ta zubar musu da ita. Wasu kwalla masu zafi ne suka zubo mai ya juya da sauri da yabar falon.

*5:03pm*

Taybah ta qarasa parlorn baqi inda saleem ke jiran ta. Tanansanye ne da atampa baby pink riga da zane sauta sa baqin hijab dinta. Ko powder babu a fukan ta balle akai ga zance kajol. Sallama tayi ciki ciki kamar wadda akasa dole. Saleem ya dago a hankali tareda amsa sallamar. Sai yaga kamar ba taybahn daya sani bace, dan ta chanja mai. Durqusawa tayi ta gaida shi sannan ta nema wuri ta zauna. Gyaran murya yayi a hankali sannan yace..."nasan kinji hukuncin da aka yanke, ni bazan iya tunkarar dad incemai bazan aureki ba. Amma zan miki kashedi guda daya, kika yadda kika bari aka kaiki gidana da sunaa....hmmmn, am sorry to say, sunnanki sorry taybah. Danni i totally hate you!". Saleem ya fada cikin wata kakkausar murya.

Wani daci taybah taji cikin ranta, to shi cemai akayi ita son nashi take? Damn him! Gashi saboda shi yanxu bazata auri wanda takeso ba.

"Yaa saleem kenan, duk abunda kaga dama kamun, i really don't give a damn! In kaga dama ka yayyanka naman jikina da dawoma iyayen namu dashi, sai lokacin zan tabbatar cewa ka tsane ni".

"Great!, yarinya zaki raina kanki kuwa". Saleem ya fada sannan a fusace ya tashi yabar dakin.

